# Jagoran Malamai

## Karatun Hausa

Aji 1




Partnership for Learning for All in Nigeria
plane

UKaid
from the British people

# Jagoran Malamai

Aji 1

## Rights and Permission

These materials were created under the Partnership for Learning for All in Nigeria (PLANE) project, funded by UK aid. These materials were adapted from materials developed under three previous UK aid funded programmes in Nigeria - the Education Sector Support Programme in Nigeria (ESSPIN), the Teacher Development Programme (TDP) as well as the Reading and Numeracy Activity (RANA) as part of the Girls' Education Project Phase 3 (GEP3) – and materials from the USAID Addressing Education in Northern Nigeria (AENN) activity. Content from these sources were streamlined into a single materials package and revised to align with the Nigerian National Curriculum and endorsed by the Kano, Kaduna and Jigawa State Governments. These materials are licensed under the Creative Commons Attribution 4.0 International license.

## Mallaka da Samarwa

An wallafa waɗannan kayan aiki ne a ƙarƙashin shirin haɗaka don samar da ilmi ga kowa da kowa, wato 'PLANE' da tallafi daga hukumar bayar da tallafi ta ƙasar Ingila, wato (UK aid). An samar da waɗannan kayan aiki ne ta hanyar 'yan sauye-sauye daga kayan aiki uku da hukumar bayar da tallafi ta ƙasar Ingila (UK aid) ta tallafa wajen aiwatar da su a Nijeriya a baya wato, tallafi ga bangaren ilimi a Nijeriya (ESSPIN) da shirin inganta malami a Nijeriya (TDP) da kuma shirin inganta karatu da lissafi (RANA) wanda aka gudanar ƙarƙashin shirin inganta ilimin 'ya'ya mata na 3 (GEP 3), sai kuma kayan aiki na shirin bunƙasa ilimi a arewacin Najeriya (AENN) wanda hukumar bayar da tallafi ta ƙasar Amurka ta yi wato, USAID. An dai tattara bayanan da aka samo daga kayayyakin aiki dabam daban da aka ambata a sama zuwa cikin wannan kundin guda ɗaya na kayan aiki wanda masana a fagen ilmi suka tabbatar da dacewarsa da tsarin manhajar koyon karatu da karantarwa ta Nijeriya sannan kuma da amincewar Gwamnatocin Jihohin Kano da Kaduna da Jigawa. Kayan aikin na da lasisi ne a ƙarƙashin tsarin bai ɗaya na mallaka mai lamba 4.0 na ƙasa da ƙasa.

# Wadanda Suka Bayar da Gudunmuwa
# (List of Contributors)

| Suna - Name | Wurin Aiki - Organisation |
|---|---|
| **Federal Partners** | |
| Nafi'u Adamu | Federal Ministry of Education, Abuja |
| Dr. Aminu Saidu | Nigerian Educational Research & Development Council |
| Abdurrazak Shehu | Universal Basic Education Board, Abuja |
| Bala M. Tatama | National Commission for Mass Literacy, Adult & Non-Formal Education |
| Auwalu Hamza | Partnership to Engage Reform and Learn (PERL), Kano |
| **Kaduna** | |
| Dr. Yahuza Salmanu | Federal College of Education, Zaria |
| Najmuddeen Alhassan | Federal College of Education, Zaria |
| Mercy B. Kude | Ministry of Education, Kaduna |
| Tanko S M Aliyu | State Universal Basic Education Board, Kaduna |
| Abubakar Umar | State Universal Basic Education Board, Kaduna |
| Pikawi Iliya Dauda | Kaduna State College of Education, Gidan Waya |
| Hauwa Maidala | Kaduna State Quality Assurance Authority |
| Garba Mohammed | LGEA Primary School, Unguwar Dankande, Igabi LGA, Kaduna |
| **Kano** | |
| Dr. Miswaru Bello | Sa'adatu Rimi College of Education, Kano |
| Zuwaira Yahaya | Sa'adatu Rimi College of Education, Kano |
| Muhammad Bello Gaya | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Mohammed Yahaya | Kano Educationa Resource Department |
| Salisu Idris | Ministry of Education, Kano |
| Amina Umar | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Munzali Mustapha | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Dr. Kabir Hamisu Kura | Community Development Initiative, Kano |
| Wasila S. Jauro | Hotoro South, Special Primary School, Kano |
| Umar Shariff Ibrahim | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Ibrahim L. Abdul | Aminu Kano College of Islamic and Legal Studies, Kano |
| Nuruddeen Dahiru | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Dr. Atika Bala | Aminu Kano College of Islamic and Legal Studies |
| Dr. Auwalu Halilu | Civil Society Coalition on Education for All (CSAFECA), Kano |
| Baffa Sale | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Tijjani Haladu B | School Based Management Committee, Kano |

| | |
|---|---|
| **Jigawa** | |
| Hamisu Iliya | State Universal Basic Education Board, Jigawa |
| Abdu Ahmed Ciroma | State Universal Basic Education Board, Jigawa |
| Dr. Sani Abdullahi | College of Education, Gumel |
| Dr. Binta U. Umar | College of Education, Gumel |
| Murtala Bala Sule | Roni Primary School, Roni |
| Habu Musa Lawal | Ministry of Education, Jigawa |
| Babangida Haruna | State Universal Basic Education Board, Jigawa |
| Arma Mohammad | Nasaro Primary School, Gumel |
| **Consultants** | |
| Dahiru Yalwa | Consultant Translator, College of Education, Azare |
| Dr. Naziru Ibrahim Abbas | Consultant Translator, Usmanu Danfodio University, Sokoto |
| Adamu Ago Saleh | Consultant Translator, Amadu Bello University, Zaria |
| Godwin Ondoma | Consultant Graphic Designer |
| Aliyu Sani Rafindadi | Consultant Graphic Designer |
| John Norj Akanbi | Consultant Illustrator |
| **PLANE Staff** | |
| Dr. Grace Bila | Inclusion Advisor, PLANE |
| Hadiza Umar | Gender Equality and Social Inclusion Specialist, PLANE |
| Lawan Ali Bukar | Technical Officer, Materials Development, PLANE Kaduna |
| Nura Garba Bakori | Technical Officer, Teacher Professional Development, PLANE Kaduna |
| Abubakar Umar | Technical Officer, Materials Development, PLANE Kano |
| Shu'aibu Mohammed Dabo | Technical Officer, Teacher Professional Development, PLANE Kano |
| Phoebe Mshelia | Technical Officer, Materials Development, PLANE Jigawa |
| Sulaiman Muhammad Bakori | Technical Officer, Teacher Professional Development, PLANE Jigawa. |
| Gabriel Yakubu | Maths Officer, PLANE Abuja |
| Zahra Abubakar Maishanu | Literacy Officer, PLANE Abuja |
| Innocent Chukwu | Monitoring and Evaluation Specialist, PLANE Abuja |
| Zainab Isah Arah | State Technical Advisor, Kano |
| Awal Mohammed | State Technical Advisor, Jigawa |
| Salim Sadiq | State Technical Advisor, Kaduna |
| Mustapha B Ahmad | State Team Lead, PLANE Jigawa |
| Lawan Umar | State Team Lead, PLANE Kano |
| Diana Agabi | State Team Lead, PLANE Kaduna |
| Caitlin Downs | HQ Technical Officer, Education |
| Edward Ishaku | Education Coordinator/ Interim Output 1 lead, PLANE |
| Emily Koester | HQ Technical Advisor, PLANE |

# Gabatarwa

An samar da wannan Jagoran Malamin ne tare da tallafin Shirin haɗaka domin bunƙasa ilmi ga kowa da kowa (PLANE), da Ofishin kula da bayar da tallafi da ci gaba na ƙasar Birtaniya (FCDO). Jihohin da a yanzu za a bai wa fifiko su ne jihohin Kano da kaduna da kuma jihar Jigawa. Har wa yau, wannan Jagorar Malamin ya samu sanya albarkar masu faɗa- a-ji a harkar ilmi tun daga matakin Gwamnatin Tarayya da na jihohi. Hukumomi kamar Majalisar gudanar da bincke da ci gaban ilmi NERDC da Hukumar lura da shirin bayar da ilmi na bai ɗaya ta ƙasa UBEC da Ma'aikatun kula da ilimi na jihohi da kuma hukumomin bayar da ilmi na bai ɗaya da ke jihohin Kano da Kaduna da Jigawa duk sun sanya wa Jogarar albarka.

## Yadda za a yi amfani da Jagoran Malamai

Wannan Jagoran Malamin na ɗauke ne da tsarin gabatar da darussan karatun Hausa a kowacce rana. Bugu da ƙari, tsarin karantar da darasin karatun Hausa da ke cikin Jagoran ya yi daidai da tsarin manhajar karantarwa da Majalisar gudanar da bincke da ci gaban ilmi ta ƙasa wato, NERDC ta amince da shi. Tsarin gabatar da darussan karatu kamar dai yadda yake ƙunshe a cikin Jagoran, yana ɗauke da tsarin darussan ne na tsawon makwanni talatin da shida (36). Haka kuma, an rarraba waɗannan darussan ne zuwa zango uku na shekarar karatu. Kowanne mako na ɗauke da adadin yawan darussa biyar. Darussan da za a gabatar a mako na shida da mako na goma sha biyu na kowanne zangon karatu sun ƙunshi waiwaye ne a kan darussan da aka gabatar a baya da kuma auna fahimtar ɗalibai.

Shi dai tsarin gudanar da darasin yana ɗauke ne da sassauƙar hanyar koyarwa da ta ƙunshi Fara darasi da yin waƙa da Koyo da Bayyanawa da Aikin Gida. Wannan tsarin yana sauƙaƙa koyo da koyarwa sannan ya samar da yanayin maimaici mai sauƙi ga dalibai.

- **Fara darasi:** Fara darasi da motsa jiki ko rera waƙa wata dabara ce ko salo na janyo hankalin ɗalibai kafin a fara aiwatar da darasin wannan rana. Irin wannan dabara ko salo kan ƙunshi rera waƙa ko wasan kacici-kaci da kuma duba aikin gidan da aka bai wa ɗalibai su yi a gida.
- **Koyo:** Ita dai wannan dabara tana taimaka wa ɗalibai ne wajan fahimtar wasu sababbin dabarun koyon karatu. Wannan tsarin koyon, malami ne ke jan linzamin gabatar da sabuwar dabarar koyon.
- **Gwaji:** Wannan salo na nuna ƙwarewa da fahimtar ɗalibai kan abin da aka koyar. Kuma yakan ba ɗaliban dama ta musamman domin su kwakwayi aiwatar da wannan sabuwar hanyar koyo kamar dai yadda malamin nasu ya/ta kwatanta musu. Salon gwajin yakan ƙunshi ɗalibai ne ke tafiyar da komai a yayin da Malami zai/za ta sanya ido ya/tana ganin abin da kowa ke yi.
- **Bayyanawa:** Wannan salon na bai wa ɗalibai damar bayyana abin da suka koya daga darasin da malami ya koyar. Hakan, zai ba Malaman zarafin gane ko ɗaliban sun fahimci darasin da aka yi ko a'a**.**
- **Aikin Gida:** Wani salo ne da Malami kan bai wa ɗalibai aiki su yi a gida. Yana da matuƙar muhimmanci Malamai su riƙa ƙarfafa wa ɗalibansu gwiwa da su riƙa yin aikin gidan da aka ba su saboda ci gaban ilmin yara yakan ta'allaƙa ne ga irin ƙarin nazari da koyo da ɗaliban kan yi bayan a tashi daga makaranta.

Muna fata wannan Jagora zai taimaka wa Malamai su riƙa gabatar da darussa nagartattu da zai ba yara damar bayar da gudumawarsu a lokacin koyar da darussa. Har wa yau, ana buƙatar Malamai su yi amfani da hikima da basirarsu don ƙara sauƙaƙa wa ɗalibai fahimtar abin da suke koyar da su.

# Muhimman Ɓangarorin koyon karatu

Tsarin karantar da kyakkyawan darasin koyon karatu na ƙunshe da ɓangarori muhimman kamar haka:

| Ɓangare | Ma'ana | Dabarun Koyarwa |
|---|---|---|
| Sanin sautukan harshe | Sauraron yadda sautukar harshe ke fitowa | • Furta wata kalma sannan a umarci ɗalibai su tafa yawan adadin gaɓar kamar yadda suka ji.<br>• Furta wata kalmomi daban-daban sannan a umarci ɗalibai su gano wata fitacciyar gaɓa daga cikin sautin gaɓoɓin da suka ji |
| Salon gano dangatakar sauti da rubutacciyar kalma | Fahimtar iya gano dangatakar da ke tsakanin sauti da rubutacciyar kalma. | • A yi amfani da katunan nune da ke ɗauke da Haruffa da Gaɓar kalmomi daban daban don auna fahimtar ɗalibai.<br>• Umarci ɗalibai su haɗa gaɓoɓin kalma daban dabam su gina kalmomi. |
| Kwarewa a Karatu | Salon iya karanta kalmomi cikin hanzari kuma daki-daki kuma su bayar da ma'ana | • Umarci ɗalibai su yi ta maimaita karanta wani labari.<br>• Karfafa wa ɗaliban gwiwa da kowannensu ya/ta karanta shi/ita kaɗai ko a rukunin mutane biyu ko fiye<br>• A bai wa ɗalibai karatun labari daban dabam domin ƙara ƙwarewa a koyon karatu. |
| Sababbin kalmomi | Fahimtar ma'anonin Sababbin/ baƙi/keɓaɓɓun kalmomi | • A koya wa ɗalibai sunaye  da ma'anar sababbi/baƙi/ keɓaɓɓun kalmomi kuma a koya musu yadda za su gano ire-irensu a cikin labari.<br>• Yi amfani da ɗaya daga cikin ire-iren waɗannan sababbi/baƙi/keɓaɓɓun kalmomi a cikin jimla sannan a umarci ɗalibai su gano ma'anarta |
| Auna Fahimta | Fahimtar abinda aka karanta | • Umarci ɗalibai su karanta wani labari sannan a yi musu tambaya a kan labarin da suka karanta.<br>• Umarci ɗalibai su karanta wani labari sannan su danganta labarin da rayuwarsu |
| Kwarewa a magana cikin harshe | Iya isar da saƙo ta hanyar magana a cikin harshe | • Umarci ɗalibai su saurara da kyau don jin labarin da za a karanto musu. Sannan sai a yi musu tambaya a kan labarin da suka ji.<br>• A nuna wa ɗalibai hoto sannan a umurci su bayyana abin da suka gani a cikin hoton. |
| Rubutu | Iya samar da rubutu mai kyau da nagarta. | • Koya wa ɗalibai yadda za su iya rubuta babban harafi da ƙaramin harafi ta yin amfani da layukan da ke cikin littafin rubutunsu.<br>• Koya wa ɗalibai yadda za su riƙa bayar da tazara a tsakanin rubutun kalma da kalma.<br>• Koya wa ɗalibai inda ake sanya aya ko alamar tambaya ko sauran alamomin rubutu. |

# *Dokoki na bai-ɗaya don shigar da dukkan ɗalibai a cikin darasi*

1. A riƙa kiran ɗalibai da sunayensu a yayin da za su amsa tambaya ko domin su gwada yin wasan kwaikwayo na wani labari.
2. A lokacin da ake zazzagayawa a cikin aji domin tallafawa ɗalibai da auna fahimtarsu, a tabbata ana sauya ɗaliban da ake tambaya a kowace rana domin a bai wa kowa dama ya faɗi amsarsa.
3. Idan ɗalibai suna shan walaha wajen fahimtar darasi, yi amfani da wasu dabarun koyarwar da za su sauƙaƙa fahimta, a kuma riƙa yabawa ɗalibai akai- akai.

## *Kai ɗauki ga buƙatun Ɗalibai*

1. ***Idan ɗalibai suna da matsalar gani (ido). Sai…***
   - *A sauya masu wurin zama zuwa gaban aji.*
   - A haɗa su da wani/wata ɗalibi/ɗaliba a matsayin aboki, wanda za su riƙa tallafa masu wajen fahimtar aikin da aka bayar kafin su fara aiwatar da aikinsu na su kaɗai.

2. ***Idan dalibai suna fama da matsalar saurare (ji) a lokacin aka ke magana da su, sai..***
   - A tabbata ana kallon ɗalibai a lokacin da ake rera waƙoƙi, kuma a daina ba su baya.
   - Umurci ɗalibai su kalli bakinka/ki a lokacin da ka/kike furta kalmomin da ke cikin waƙar.
   - A nuna hoton da ke jikin waƙar domin taimaka wa ɗalibai su fahimci abin da waƙar ta ƙunsa.

3. ***Idan ɗalibai suna buƙatar ƙarin taimako da zai sa su kewaya a cikin ajin, sai….***
   - A taƙaita neman kayan aikin a muhallin da ɗalibai suke.
   - Ɗalibai za su iya jagorantar rera waƙa a lokacin da aikin ke gudana daga kowane ɓangare na ajin. Ɗaliban da ke jagorantar waƙar za su tsaya a rukuninsu yayin da sauran ɗaliban ajin za su juya fuskokinsu gare su.
   - A riƙa zagayawa a cikin aji a lokacin da ake koyarwa. Duk da cewa Allo yana gaban aji, ba tilas bane kowane gwaji da malami zai yi sai ya kasance a gaban allo ba.

4. ***Idan ɗalibai suna buƙatar ƙarin tallafi domin mayar da hankali ga aikin da aka basu. Sai…***
   - A jawo hankalinsu zuwa ga allo, a kan duk wani zane ko hoton da zai tallafawa darasin.
   - A lokacin rera waƙa, nuna kowace kalma ko hoto da ke da alaƙa da waƙar, musamman a yayin rera sabuwar waƙa a karon farko.
   - A bai wa ɗaliban da ba sa mayar da hankali wani aiki na musamman a cikin aji ko a rukuninsu domin ƙarfafarsu su mayar da hankali a kan aikin aji.
   - A karfafa haɗa ɗalibai ƙanana da manya wuri ɗaya, domin su tallafa masu shiga a cikin aikin da aka ba su.

# Zango na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **N n**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta (Minti 5)

Ⓜ
- Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

MD
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu.

A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

**N n**

Ⓜ
- Rubuta **N n** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***N.***
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***N****, kamar a cikin kalmar* ***noma. Noma, noma, noma!***

MD
- Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **6** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Nafisa da Nura*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***N****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **N** da ke ciki.

### Gwaji



4. Haɗa haruffa (Minti 10)

Ⓜ
- Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **N n** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

MD
- Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

### Bayyanawa

5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **N n** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **N n**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

Ⓜ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

**N n**

Ⓜ • Rubuta **N n** a kan allo.
ⓂⒹ • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin **N**, kamar a cikin kalmar: **noma. Noma, noma, noma!***
• **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da **N**. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Kalmar **noma** na farawa da harafin **n**. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin **n**?*
• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **n** da ke ciki.

## Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 15)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
• Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **N** tare da yin bayanin matakan rubutun.
ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **n**.
Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
• Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

• Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
• Idan akwai sauran lokaci, a zabi wani labari a karanta wa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 1 | Mako na 3 | Darasi na 3 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **N**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **N** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"na"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **nama, tsalle, nakiya, nasara, rawa.**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***6***.
- Rubuta: **na**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓar kalmar **an.**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

**n** **a**

- Nuna katuna ɗauke da haruffan **n** da **a**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Rubutun gaɓar kalma (Minti 10)

- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta gaɓar kalmar **na.**
- Umurci ɗalibai da su rubuta gaɓar kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
- Maimaita waɗannan matakan da gaɓar kalmar **na.**

**Bayyanawa**

7. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 1 | Mako na 3 | Darasi na 4 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **N**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
(D) • Umurci ɗalibai da su gano harafin **N** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

(MD) • **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku:* **Nana, noma, Nafisa, nama**

4. Karatun kalma (Minti 10)

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***6****.*
• Rubuta: **Nana**
• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
(D) • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
(M) • Maimaita waɗannan matakan da ana. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 10)

na na
a na

(MD) • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
(D) • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

**Bayyanawa**

6. Bayyana fahimta (Minti 2)

• Ka/ki ce: *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.
• Ka/ki ce: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

(MD) • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 1 | Mako na 3 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| n | a |
| N | n |

| | |
|---|---|
| an | a |
| na | na |

| | |
|---|---|
| ana | Nana |
| Nana | na |

### Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

| No. 6 | Zango na 1 | Mako na 4 | Darasi na 1 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **K k**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta Tsafta (Minti 5)

Ⓜ
- Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD)
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

K k

Ⓜ
- Rubuta **K k** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***K***.
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***K****, kamar a cikin kalmar* ***kama. Kama, kama, kama!***

(MD)
- Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **8** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Kabiru da Karima*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***K****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **K** da ke ciki.

## Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)

K k

Ⓜ
- Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **K k** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD)
- Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **K k** da wake ko duwatsu a gida.

## No. 7 | Zango na 1 | Mako na 4 | Darasi na 2

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **K k**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu    **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta Tsafta (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

K k

- Rubuta **K k** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***K****, kamar a cikin kalmar:* ***kama. Kama, kama, kama!***
- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***K****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***kaza*** *na farawa da harafin* ***k****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***k****?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **k** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **K** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Maimaita waɗannan matakan da harafin **k**.
- Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 1 Mako na 4 Darasi na 3

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **K**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tsafta Tsafta (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

• Umurci ɗalibai da su gano harafin **K** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜ︎Ⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"ka"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **ƙwallo, kaka, kakaki, ayaba, kankana**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***8***.
• Rubuta: **ka**
• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.

Ⓜ︎Ⓓ • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.

Ⓜ • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓar kalmar **na.**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

| k | a |
|---|---|

Ⓜ︎Ⓓ • Nuna katuna ɗauke da haruffan **k** da **a**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.

Ⓓ • Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.

• Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Rubutun gaɓar kalma (Minti 10)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta gaɓar kalmar **ka.**

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta gaɓar kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da gaɓar kalmar **na.**

**Bayyanawa**

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta gaɓoɓin kalmar a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 1 Mako na 4 Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **K**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Tafa Tafa (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **K** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓobin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **Kaka, kakaki, kaza, kare**

4. Karatun kalma (Minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓobin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na **8**.*
- Rubuta: **kaka**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- Maimaita waɗannan matakan da **kana, naka**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 10)

ka | ka
na | na

- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Bayyanawa

6. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 1 | Mako na 4 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Tafa Tafa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

3. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| K | k |
| a | A |

| | |
|---|---|
| an | ka |
| ka | na |

| | |
|---|---|
| kaka | kaka |
| kana | naka |

### Saurare

4. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ 5. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.
• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **M m**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

M m

Ⓜ • Rubuta **M m** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***M.***
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***M****, kamar a kukan saniya* ***moow. Moow, moow, moow!***

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **10** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Musa da Maryam*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***M****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **M** da ke ciki.

## Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **M m** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **M m** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **M m**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)

- Ⓜⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

M m

- Ⓜ Rubuta **M m** a kan allo.
- Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***M****, kamar a kukan saniya:* ***moow. Moow, moow, moow!***
- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***M****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- Ⓓ **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***masa*** *na farawa da harafin* ***m****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***m****?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **m** da ke ciki.

## Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- Ⓜ Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **M** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- Ⓜⓓ Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- Ⓓ Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Ⓜ Maimaita waɗannan matakan da harafin **m**.
- Ⓓ Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 1 | Mako na 5 | Darasi na 3 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **M**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **M** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* **"ma"** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **masa, tauraro, sama, masara, taɓarya**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***10***.
- Rubuta: **ma**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **am, na.**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| m | a |
|---|---|

- Nuna katuna ɗauke da haruffan **m** da **a**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Rubutun gaɓar kalma (Minti 10)

- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta gaɓar kalmar **ma.**
- Umurci ɗalibai da su rubuta gaɓar kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
- Maimaita waɗannan matakan da gaɓar kalmar **am, na.**

### Bayyanawa

7. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta gaɓoɓin kalmar a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 1 Mako na 5 Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **M**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)

Ⓜⓓ
- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **M** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

3. *Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **masa, mama, makaranta, masara**

4. Karatun kalma (Minti 10)

Ⓜ
- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na **10**.*
- Rubuta: **mama**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.

Ⓜ
- Maimaita waɗannan matakan da **amma, nama**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| ma | ma |
| am | na |

Ⓜⓓ
- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Bayyanawa

6. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

Ⓜⓓ
- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 9 | Zango na 1 — Mako na 5 — Darasi na 5

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

3. Bita da gwaji (Minti 12)

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

(MD) • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

(D) • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| A | N |
| n | M |

| | |
|---|---|
| am | am |
| ma | na |

| | |
|---|---|
| mama | nama |
Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ 5. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

| **No. 6** | **Zango na 2** | **Mako na 4** | **Darasi na 1** |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **G g**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.

**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Gizo (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

• Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

**G g**

Ⓜ • Rubuta **G g** a kan allo.

• **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***G****.*

• A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***G****, kamar a cikin kalmar* ***gudu. Gudu, gudu, gudu!***

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.

• Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **33** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.

• ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Garba da Gazali*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***G****?*

• Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **G** da ke ciki.

## Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **G g** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.

• Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.

• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **G g** da wake ko duwatsu a gida.

## No. 7 | Zango na 2 Mako na 4 Darasi na 2

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **G g**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Gizo (Minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

**G g**

- Ⓜ • Rubuta **G g** a kan allo.
- Ⓜ︎Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* **G**, *kamar a cikin kalmar:* ***gudu. Gudu, gudu, gudu!***
- • **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* **G**. *A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***gida*** *na farawa da harafin* **g**. *Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* **g**?
- • Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **g** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- • Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **G** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **g**.
- Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- • Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **G**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Gizo (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **G** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"gi"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **'yan'uwa, gida, maƙota, gini, dangi**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***33***.
- Rubuta: **ga**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **gan, gi.**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7) **g** **i**

- Nuna katuna ɗauke da haruffan **g** da **i**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***33****.*
- Rubuta: **gasa**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- Maimaita waɗannan matakan da **ganga, gida**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Bayyanawa

7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**No. 8 | Zango na 2 — Mako na 4 — Darasi na 4**

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **G**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Gizo (Minti 3)

Ⓜⓓ
- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **G** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

**Koyo**

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **gajimare, ganga, gizo, gatari**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| ga | sa |
| gan | na |

Ⓜ
- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

**Gwaji**

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ
- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **ganga.**

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

Ⓜ
- Maimaita waɗannan matakan da kalmar **gasa.**

**Bayyanawa**

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

Ⓜⓓ
- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Gizo (Minti 3)

- Ⓜⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

3. Bita da gwaji (Minti 12)

- Ⓜ **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*
- Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.
- Ⓜⓓ Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.
- Ⓓ Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| g i<br>I G | gi ga<br>gan gi |

| |
|---|
| gasa gida<br>ganga ganga |

## Saurare

4. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

- Ⓜ Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.
- Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.
- Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 5. Auna fahimta (Minti 7)

- A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.
- A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.
- A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

- Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.
- Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **Y y**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tsafta (Minti 5)

(M) • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 10)

Y y

(M) • Rubuta **Y y** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **Y**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **Y**, kamar a cikin kalmar **yanka. Yanka, yanka, yanka!***

(MD) • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

(D) • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **35** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce**: Sunayen **Yakubu da Yasira** na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin **Y**?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **Y** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



(M) • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **Y y** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD) • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

(D) • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)
- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **Y y** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **Y y**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

- Ⓜⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 6)

Y y

- Ⓜ Rubuta **Y y** a kan allo.
- Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***Y****, kamar a cikin kalmar:* ***yanka. Yanka, yanka, yanka!***
- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***Y****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- Ⓓ **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***yara*** *na farawa da harafin* ***y****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***y****?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **y** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- Ⓜ Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **Y** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- Ⓜⓓ Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- Ⓓ Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Ⓜ Maimaita waɗannan matakan da harafin **y**.
- Ⓓ Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **Y**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **Y** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

## Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜ︎Ⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* **"ya"** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **yara, tantabara, yanayi, bishiya, yarinya**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- Ⓜ︎ **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***35***.
- Rubuta: **yi**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- Ⓜ︎Ⓓ Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- Ⓜ︎ A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **ya, yan.**

## Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| y | i |
|---|---|

- Ⓜ︎Ⓓ Nuna katuna ɗauke da haruffan **y** da **i**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Ⓓ Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- Ⓜ︎ **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaboɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***35***.
- Rubuta: **yayi**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- Ⓜ︎Ⓓ Ⓓ Maimaita waɗannan matakan da **yadi, yanka**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

## Bayyanawa

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 2 Mako na 5 Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **Y**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **Y** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓobin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **yanayi, yau, yanka, yamma**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| yan | ka |
| ya | yi |

- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **yayi.**
- Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
- Maimaita waɗannan matakan da kalmar **yanka.**

### Bayyanawa

6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 2 | Mako na 5 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Tsafta (Minti 3)

ⓂⒹ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

3. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

ⓂⒹ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| Y K | yan yan |
| K y | yi ya |

| | |
|---|---|
| yadi | yayi |
| yayi | yanka |

## Saurare

4. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 5. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

| No. 31 | Zango na 2 | Mako na 6 | Darasi na 1 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su karanta da kuma rubuta haruffan **Ts ts B b W w G g Y y**
**Kayan aiki:** Fensira da littafan rubutu **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (minti 5)

Ⓜⓓ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.

• Faɗi wasu haruffa da ɗalibai suka koya, a umurce su da su nuna su a cikin waƙar.

**Bita**

✓ 2. Bitar haruffa (minti 12):

**Ts ts B b W w G g Y y**

Ⓜ • Rubuta waɗannan haruffan a kan allo:
**Ts ts B b W w G g Y y**

• **Ka/ki ce:** *A yau zamu yi gwaji da bitar haruffan da muka koya a baya.*

Ⓓ • Nuna kowane harafi a jere. Umurci ɗalibai su karanta kuma su nuna harafin. Ba ɗalibai dama su faɗi sunan harafin kafin ka/ki karanta.

• Nuna harruffan ba a cikin jeri ba, sannan a umurci ɗalibai da su karanta su.

• Umurci ɗalibai su yi motsin jikin kowane harafin.

• Umurci ɗalibai su faɗi sunayen da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allo.

• Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allon.

**Gwaji**

3. Rubutu (minti 13)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo. Rubuta manya da ƙananan haruffan guda biyar. Yi bayanin matakan da ake bi yayin rubutun. Yi wa ɗalibai bayani cewa tsayin ƙaramin harafi yakan kasance rabin babban harafin.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a cikin littafan rubutunsu. Zagaya domin ba su taimako.

**Bayyanawa**

✓ 4. Bayyana fahimta (minti 5)

• Nuna wa ɗalibai rubutun 'yan uwansu da suka yi da kyau, a kuma yi musu bayanin dalilin da ya sa rubutun ya yi kyau.

• Furta sunan harafi. Umurci ɗalibai da su nuna shi a cikin littafin rubutunsu. Maimata hakan da sauran haruffan.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su sake rubuta haruffan a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 32 | Zango na 2 | Mako na 6 | Darasi na 2 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su karanta gaɓoɓin kalma da kalmomin da ke ɗauke da haruffan **Ts B W G Y**

**Kayan aiki:** Littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (minti 3)

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da motsin jikin waƙar.

(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (minti 4)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kamala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Gwaji da bita (minti 7):

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar karatun gaɓoɓin kalma da kuma kalmomi.*

• Rubuta rukunin gaɓoɓin kalma da kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla gaɓar kalma ko kalma ɗaya na da ’yar’uwa a cikin akwatin.

(D) • Nuna kowace sannan a nemi ɗalibai da su karanta su.

• Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | | |
|---|---|---|
| ba | tsi | wa |
| yi | ba | ga |

| | | |
|---|---|---|
| kana | Nana | kan |
| naka | kana | nama |

**Gwaji**

4. Katunan nune: dukkan aji (minti 5)

(MD) • Nuna katunan nune. Umurci ɗalibai su karanta gaɓar da ke jiki.

• Haɗa katunan, domin samar da kalma. Umurci ɗalibai da su karanta kalmar da aka samar.

(D) • Kira ɗalibai su fito a ra’ayin kansu a gaban aji, su haɗa kalmomi daga katunan.

| | |
|---|---|
| wa | sa |
| ga | ta |

5. Katunan nune: ƙananan rukunai (minti 10)

(D) • Umurci ɗalibai da su zauna a cikin ƙananan rukunai. Raba wa kowane rukuni ƙananan takardu guda huɗu masu ɗauke da gaɓoɓin kalma. A umurce su da su haɗa kalmomi daga katunan.

**Bayyanawa**

✓ 6. Bayyana fahimta (minti 5)

Umurci kowane rukuni da ya gabatar da kalma ɗaya da ya haɗa daga katunan nune.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta kalmomi huɗu a cikin littafan rubutunsu.

## No. 33 | Zango na 2 Mako na 6 Darasi na 3

**Manufofi:** Ɗalibai su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki su kuma saurari labari.
**Kayan Aiki:** Littafin karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

<u>1. Waƙar Haruffa (Minti 3)</u>

- Rera waƙar da ɗalibai tare da nuna kalmomin waƙar.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmomin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.

<u>2. Duba aikin gida (Minti 3)</u>

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

<u>3. Kalmomin aiki (Minti 10)</u>

- Rubuta: **buɗe ɗauko ɗauki wanke zauna ci**
- Ka/ki ce: *Yau za mu koyi kalmomin aiki. Za mu karanta kowace kalma tare. Bayan mun karanta kowace kalma, za ku kwatanta aiwatar da ma'anar wannan kalmar.*
- Umurci ɗalibai da su miƙe tsaye. A tallafa musu yadda za su aiwatar da ma'anar kowacce kalma.
- Kira ɗaya daga cikin ɗaliban zuwa gaban allo. Umurci da ya/ta zaɓi kalma ɗaya daga cikin jerin kalmomin ya/ta aiwatar da ma'anar kalmar ba tare da karanta ta ba.
- Sauran ɗalibai za su canki wace kalma ce ake kwatantawa. A maimata da wasu ɗalibai na daban.

### Gwaji

<u>4. **Labari a kan tsafta** (Minti 10)</u>

- **Ka/ki ce**: *A yau za mu karanta wani labari. Ku buɗe littafinku zuwa shafi na **37**.*
- **Ka/ki ce:** *Me kuka gani a cikin hoton*?
- **Ka/ki ce:** *Me kuke tunanin labarin zai kunsa?*
- **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomi kuka gane?*
- Karanta wa ɗalibai labarin sau ɗaya.
- Sake karanta labarin a bayyane. Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu a duk lokacin da suka ji kalmar aiki.

### Bayyanawa

<u>5. Auna fahimta (Minti 5)</u>

**Ka/ki ce:**

- ***Wa ya je banɗaki?***
- ***Me ya sa Sani ya wanke hannayensa?***
- ***Ta yaya za ku iya tabbatar da tsabtar jikinku?***

### Aikin Gida

Nemi ɗalibai da su ba 'yan'uwansu ko abokai labarin da aka karanto musu.

| No. 34 | Zango na 2 | Mako na 6 | Darasi na 4 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki, su kuma kwaikwayi labari.
**Kayan aiki:** Littafin ɗalibai **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (minti 5)

- ⓂⒹ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

### Koyo

✓ 2. Kalmomin aiki (minti 10)

- ⓂⒹ **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomin aiki muka koya a darasin jiya?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo.
- Ⓓ Umurci ɗalibai da su karanta dukkanin kalmomin, su kuma kwatantasu.
- Kira ɗaya daga cikin ɗalibai gaban aji, domin zaɓen kalma ɗaya a kwatanta ta ba tare da karanta kalmar ba. Maimaita da waɗansu ɗaliban na daban.

3. Baƙin k almomi (minti 5)

- Ⓜ Rubuta: **[tsafta]**
- ⓂⒹ Umurci ɗalibai da su ba da ma'anar kalmar tare da misalai. A taimakawa ɗalibai idan sun kasa.
- Ⓓ A tambayi ɗalibai muhimmancin **tsafta**.

### Gwaji

5. Labari a kan tsafta (minti 10)

- Ⓓ Umurci ɗalibai da su ba da labarin da aka karanto a darasin da ya gabata.
- ⓂⒹ Kira ɗalibai domin su kwatanta abin da ke faruwa a labarin, yayin da ka/kike sake karanta labarin.
- Kira waɗansu ɗaliban na daban domin su ma su kwatanta abin da ke faruwa a labarin yayin da ka/kike karantawa.
- Ⓓ Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin aiki da ke cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (minti 10)

**Ka/ki ce:**

- ***Wa ya je banɗaki?***
- ***Me ya sa Sani ya wanke hannayensa?***
- ***Ta yaya za ku iya tabbatar da tsabtar jikinku?***

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su zana hoton labarin a littafansu na rubutu.

| No. 35 | Zango na 2 | Mako na 6 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

Manufofi: Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar jarrabawar koyon karatu.
Kayan Aiki: Littafin ɗaukar bayanai da takardar karatu. Lokaci: Minti 35

**JARRABAWA**

Kira ɗalibai ɗaya bayan ɗaya, a yi musu tambayoyi sannan a rubuta sakamakon kowannensu a littafin ɗaukar bayanai. Idan da buƙata, ka/ki nemi tallafi daga Shugaban Makaranta ko 'yan kwamitin 'SBMC' ko daga sauran malamai domin tafiyar da aikin.

Ba wa sauran ɗalibai wani aiki yayin da suke jiran a yi musu jarrabawar. Alal-misali, za a iya ba ɗalibai wani abu su rubuta domin ƙara ƙwarewa wajen rubutu, ko su zana waɗansu abubuwa.

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan haruffa (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**ts G y b B**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan gaɓoɓin kalma (A bayar da maki ɗaya kan kowace gaɓar kalma da aka karanta daidai)

**ba gi tsa yi wa**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan kalmomi (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**wanka tsani ganga yayi Baba**

# Zango na 2, Mako na 6 – Jarrabawar tsakiyar Zango

| **Jaha:** | | **Karamar Hukuma:** | | **Makaranta:** | | **Wata:** | | **Shekara:** | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|

| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Bukata ta Musamman (Eh/A'a) | Haruffa | Gaɓar Kalma | Kalma | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /5 | /5 | /5 | / 15 |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |

## No. 6 | Zango na 2 Mako na 7 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[L l]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 10)

L l

Ⓜ • Rubuta **[L l]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **[L]**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **[L]**, kamar a cikin kalmar **[leƙa. Leƙa, leƙa, leƙa!]***

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[39]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce**: Sunayen **Larai da Lawal** na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin **[L]**?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[L]** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 14)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[L]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[l]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[L l]** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[U u]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 10)

U u

Ⓜ • Rubuta **[U u]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***[U]***.
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***[U]****, kamar a cikin kalmar* ***[ungo. Ungo, ungo, ungo!]***

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[39]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Ubaida da Usman*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***[U]****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[U]** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 14)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[U]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[u]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)
- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 2 | Mako na 7 | Darasi na 3 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[L]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
• Umurci ɗalibai da su gano harafin **[L]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* **"lu"** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **damina, lura, lalura, ranaku, lumana**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[39]***.
• Rubuta: **[lu]**
• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
(MD) • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
(M) • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[la, lan].**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

(MD) • Nuna katuna ɗauke da haruffan **[l]** da **[u]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi. l u
(D) • Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
• Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[39]****.*
• Rubuta: **[lumana]**
• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
(D) • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
(M) • Maimaita waɗannan matakan da **[ulu, langa]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

**Bayyanawa**

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 2    Mako na 7    Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[L]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
(D) • Umurci ɗalibai da su gano harafin **[L]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaboɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **lada, langa, lumana, lambu**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| u | lu |
|---|---|
| lan | ga |

(MD) • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
(D) • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

(MD) • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[ulu].**
(D) • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
(M) • Maimaita waɗannan matakan da kalmar **[langa].**

### Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

(MD) • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
• **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ️Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜ️Ⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| u L<br>I U | la lan<br>lu lu |

| |
|---|
| ulu lumana<br>langa ulu |

## Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

6. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a ciki. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 6 | Zango na 2 Mako na 8 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **C c**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
• Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

C c

Ⓜ • Rubuta **C c** a kan allo.
• **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***C.***
• A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **C**, kamar a cikin kalmar **ci. Ci, ci, ci!***

(MD) • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
• Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **41** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
• ***Ka/ki ce****: Sunayen **Cika da Curi** na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin **C**?*
• Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **C** da ke ciki.

### Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **C c** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD) • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
• Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **C c** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **C c**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

C c

- Ⓜ Rubuta **C c** a kan allo.
- Ⓜ︎Ⓓ **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***C****, kamar a cikin kalmar:* ***ci. Ci, ci, ci!***
- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***C****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- Ⓓ **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***ciki*** *na farawa da harafin* ***c****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***c****?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **c** da ke ciki.

## Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- Ⓜ Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **C** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- Ⓜ︎Ⓓ Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- Ⓓ Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Ⓜ Maimaita waɗannan matakan da harafin **c**.
- Ⓓ Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **C**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta rika nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
• Umurci ɗalibai da su gano harafin **C** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

## Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"ci"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **abinci, ciki, nama, ciniki, tuwo**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***41***.
• Rubuta: **ci**
• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
Ⓜⓓ • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
Ⓜ • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **kin, cin.**

## Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| c | i |
|---|---|

Ⓜⓓ • Nuna katuna ɗauke da haruffan **c** da **i**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
Ⓓ • Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
• Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***41***.
• Rubuta: **cikin**
• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da **cinnaka, abinci**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

## Bayyanawa

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No.8 | Zango na 2 Mako na 8 Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **C**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

ⓂⒹ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su gano harafin **C** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

ⓂⒹ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **ciniki, ci, ciki, ciyarwa**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| a | bin |
| ci | kin |

Ⓜ • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **cikin.**
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da kalmar **abinci.**

### Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

ⓂⒹ • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
• **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 2 | Mako na 8 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

- Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜ︎Ⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| C N<br>n c | ci ci<br>cin kin |

| |
|---|
| cikin abinci<br>cinnaka cinnaka |

## Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.

- Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.
- Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

- A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.
- A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.
- A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

- Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.
- Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 6 | Zango na 2 Mako na 9 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **H h**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Kirge (Minti 5)

- Ⓜ Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- (MD) Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

H h

- Ⓜ Rubuta **H h** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **H**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **H**, kamar a cikin kalmar **hamma. Hamma, hamma, hamma!***
- (MD) Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.
- Ⓓ Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **43** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce**: Sunayen **Habibu da Hadiza** na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin **H**?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **H** da ke ciki.

### Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



- Ⓜ Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **H h** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.
- (MD) Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.
- Ⓓ Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **H h** da wake ko duwatsu a gida.

## No. 7 | Zango na 2 — Mako na 9 — Darasi na 2

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **H h**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu — Lokaci**:** Minti 35

### Fara Darasi

<u>1. Waƙar Kirge (Minti 3)</u>

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ <u>2. Duba aikin gida (Minti 1)</u>

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

<u>3. Sunan harafi (Minti 6)</u>

H h

(M) • Rubuta **H h** a kan allo.

(MD) • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***H****, kamar a cikin kalmar:* ***hamma. Hamma, hamma, hamma!***

- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***H****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*

(D) • **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***hira*** *na farawa da harafin* ***h****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***h****?*

- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **h** da ke ciki.

### Gwaji

<u>4. Rubutun harafi (Minti 15)</u>

(M) • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.

- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **H** tare da yin bayanin matakan rubutun.

(MD) • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

(D) • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

(M) • Maimaita waɗannan matakan da harafin **h**.

(D) • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.

- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

✓ <u>5. Bayyana fahimta (Minti 10)</u>

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zabi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **H**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- (MD) Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- (D) Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **H** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

## Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"hu"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **hutu, hula, unguwa, gwanda, hukunci**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- (M) **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***43***.
- Rubuta: **hu**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- (MD) Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- (M) A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **tu, han.**

## Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| h | u |
|---|---|

- (MD) Nuna katuna ɗauke da haruffan **h** da **u**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- (D) Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- (M) **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***43***.
- Rubuta: **hutu**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- (D) Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- (M) Maimaita waɗannan matakan da **hula, hannu**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

## Bayyanawa

7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 2 Mako na 9 Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **H**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Kirge (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su gano harafin **H** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

ⓂⒹ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **hukuma, hula, huhu, hutu**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| hu | tu |
|---|---|
| la | han |

ⓂⒹ • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **hannu.**

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
- Maimaita waɗannan matakan da kalmar **hutu.**

### Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

ⓂⒹ • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Kirge (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

3. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| u h | han tu |
| H U | hu hu |

| | |
|---|---|
| hutu | hula |
| hula | hannu |

## Saurare

4. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 5. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 6 | Zango na 2 Mako na 10 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **Sh sh**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
• Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Sh sh

Ⓜ • Rubuta **Sh sh** a kan allo.
• **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **Sh**.*
• A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **Sh**, kamar a cikin kalmar **shiru. Shiru, shiru, shiru!***

(MD) • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
• Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **45** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
• ***Ka/ki ce**: Sunayen **Shehu da Shamsiya** na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin **Sh**?*
• Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **Sh** da ke ciki.

### Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)

Sh sh

Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **Sh sh** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD) • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
• Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **Sh sh** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **Sh sh**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

Sh sh

Ⓜ • Rubuta **Sh sh** a kan allo.

Ⓜⓓ • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***Sh****, kamar a cikin kalmar:* ***shiru. Shiru, shiru, shiru!***

• **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***Sh****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*

Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***shanu*** *na farawa da harafin* ***sh****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***sh****?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **sh** da ke ciki.

## Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.

• Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **Sh** tare da yin bayanin matakan rubutun.

Ⓜⓓ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **sh**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.

• Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

• Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.

• Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.

• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 2 Mako na 10 Darasi na 3

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **Sh**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **Sh** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* **"shu"** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **shuka, tuƙi, katuna, shuni, shuɗi**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***45***.
- Rubuta: **sha**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **shi, ru.**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| sh | a |
|---|---|

- Nuna katuna ɗauke da haruffan **sh** da **a**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***45***.
- Rubuta: **shayi**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- Maimaita waɗannan matakan da **shan, shiru**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Bayyanawa

7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 2 Mako na 10 Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **Sh**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

<u>1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)</u>

(MD)
- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

(D)
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **Sh** a cikin waƙar.

(✓) <u>2. Duba aikin gida (Minti 3)</u>

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

<u>*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)</u>

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **shinkafa, shiru, shahararre, shayi**

| sha | yi |
|---|---|
| shi | ru |

<u>4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)</u>

(M)
- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

(D)
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

<u>5. Rubutun kalma (Minti 10)</u>

(M)
- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **shan.**

(D)
- Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

(M)
- Maimaita waɗannan matakan da kalmar **shiru.**

### Bayyanawa

(✓) <u>6. Bayyana fahimta (Minti 5)</u>

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

<u>7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)</u>

(MD)
- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Gaisuwa (Minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

- Ⓜ **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*
- Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.
- Ⓜ︎Ⓓ Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.
- Ⓓ Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| Y y<br>Sh sh | shi Sha<br>sha ru |
|---|---|

| shayi shayi<br>shan shiru |
|---|

## Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

- Ⓜ Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.
- Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.
- Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

- A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.
- A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.
- A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

- Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.
- Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **F f**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tafa Tafa (Minti 5)

Ⓜ
- Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 10)

F f

Ⓜ
- Rubuta **F f** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **F**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **F**, kamar a cikin kalmar **fere. Fere, fere, fere!***

ⓂⒹ
- Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **47** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce**: Sunayen **Faisal da Fatima** na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin **F**?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **F** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ
- Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **F f** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

ⓂⒹ
- Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **F f** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **F f**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tafa Tafa (Minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 6)

F f

- Ⓜ Rubuta **F f** a kan allo.
- Ⓜ︎Ⓓ **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***F****, kamar a cikin kalmar:* ***fere. Fere, fere, fere!***
- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***F****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- Ⓓ **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***fadama*** *na farawa da harafin* ***f****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***f****?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **f** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- Ⓜ Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **F** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- Ⓜ︎Ⓓ Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- Ⓓ Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Ⓜ Maimaita waɗannan matakan da harafin **f**.
- Ⓓ Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 2 | Mako na 11 | Darasi na 3 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **F**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Tafa Tafa (Minti 3)

- (MD) Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- (D) Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **F** a cikin waƙar.

(✓) 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"fu"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **mota, fura, fure, kakkarwa, fulani**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- (M) **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***47***.
- Rubuta: **fa**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- (MD) Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- (M) A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **ra, da.**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| f | a |
|---|---|

- (MD) Nuna katuna ɗauke da haruffan **f** da **a**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- (D) Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- (M) **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***47****.*
- Rubuta: **fara**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- (D) Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- (M) Maimaita waɗannan matakan da **dafa, fadawa**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Bayyanawa

(✓) 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **F**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Tafa Tafa (Minti 3)

Ⓜⓓ
- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **F** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

**Koyo**

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **fartanya, fari, fahimta, farinciki**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| fa | ra |
| da | wa |

Ⓜ
- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

**Gwaji**

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ
- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **dafa.**

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

Ⓜ
- Maimaita waɗannan matakan da kalmar **fara.**

**Bayyanawa**

6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Tafa Tafa (Minti 3)

Ⓜ️Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜ️Ⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| d D<br>F f | fa fa<br>ra da |

| |
|---|
| ɗafa fara<br>fara fadawa |

## Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abin da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abin da suka ji ko kuma abin da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abin da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 31 | Zango na 2 Mako na 12 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su karanta da kuma rubuta haruffan **Ll Uu Cc Hh Sh sh Ff**
**Kayan aiki:** Fensira da littafan rubutu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (minti 5)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.

• Faɗi wasu haruffa da ɗalibai suka koya, a umurce su da su nuna su a cikin waƙar.

### Bita

2. Bitar haruffa (minti 12)

**Ll Uu Cc Hh Sh sh Ff**

Ⓜ • Rubuta waɗannan haruffan a kan allo:
**Ll Uu Cc Hh Sh sh Ff**

• **Ka/ki ce:** *A yau zamu yi gwaji da bitar haruffan da muka koya a baya.*

Ⓓ • Nuna kowane harafi a jere. Umurci ɗalibai su karanta kuma su nuna harafin. Ba ɗalibai dama su faɗi sunan harafin kafin ka/ki karanta.

• Nuna harruffan ba a cikin jeri ba, sannan a umurci ɗalibai da su karanta su.

• Umurci ɗalibai su yi motsin jikin kowane harafin.

• Umurci ɗalibai su faɗi sunayen da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allo.

• Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allon.

### Gwaji

3. Rubutu (minti 13)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo. Rubuta manya da ƙananan haruffan guda shida. Yi bayanin matakan da ake bi yayin rubutun. Yi wa ɗalibai bayani cewa tsayin ƙaramin harafi yakan kasance rabin babban harafin.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a cikin littafan rubutunsu. Zagaya domin ba su taimako.

### Bayyanawa

✓ 4. Bayyana fahimta (minti 5)

• Nuna wa ɗalibai rubutun 'yan uwansu da suka yi da kyau, a kuma yi musu bayanin dalilin da ya sa rubutun ya yi kyau.

• Furta sunan harafi. Umurci ɗalibai da su nuna shi a cikin littafin rubutunsu. Maimata hakan da sauran haruffan.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su sake rubuta haruffan a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 32 | Zango na 2 | Mako na 12 | Darasi na 2 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su karanta gaɓoɓin kalma da kalmomin da ke ɗauke da haruffan **L U C H Sh F**

**Kayan aiki:** Littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar da ɗalibai tare da motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (minti 4)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kamala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

2. Gwaji da bita (minti 7):

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar karatun gaɓoɓin kalma da kuma kalmomi.*

• Rubuta rukunin gaɓoɓin kalma da kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla gaɓar kalma ko kalma ɗaya na da 'yar'uwa a cikin akwatin.

Ⓓ • Nuna kowace sannan a nemi ɗalibai da su karanta su.

• Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | | |
|---|---|---|
| fa | hu | sha |
| cin | hu | lu |

| | | |
|---|---|---|
| hula | ulu | shayi |
| cikin | kana | fara |

**Gwaji**

5. Katunan nune: dukkan aji (minti 5)

| | |
|---|---|
| shi | ru |
| ci | kin |

Ⓜ︎Ⓓ • Nuna katunan nune. Umurci ɗalibai su karanta gaɓar da ke jiki.

• Haɗa katunan, domin samar da kalma. Umurci ɗalibai da su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu a gaban aji, su haɗa kalmomi daga katunan.

6. Katunan nune: ƙananan rukunai (minti 10)

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su zauna a cikin ƙananan rukunai. Raba wa kowane rukuni ƙananan takardu guda huɗu masu ɗauke da gaɓoɓin kalma. A umurce su da su haɗa kalmomi daga katunan.

**Bayyanawa**

✓ 7. Bayyana fahimta (minti 5)

Umurci kowane rukuni da ya gabatar da kalma ɗaya da ya haɗa daga katunan nune.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta kalmomi huɗu a cikin littafan rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki su kuma saurari labari.

**Kayan Aiki:** Littafin karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar da ɗalibai tare da nuna kalmomin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmomin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Kalmomin aiki (Minti 10)

Ⓜ • Rubuta: **wanke taya bitar ziyartar hutawa**

- Ka/ki ce: *Yau za mu koyi kalmomin aiki. Za mu karanta kowace kalma tare. Bayan mun karanta kowace kalma, za ku kwatanta aiwatar da ma'anar wannan kalmar.*

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su miƙe tsaye. A tallafa musu yadda za su aiwatar da ma'anar kowacce kalma.

- Kira ɗaya daga cikin ɗaliban zuwa gaban allo. Umurci da ya/ta zaɓi kalma ɗaya daga cikin jerin kalmomin ya/ta aiwatar da ma'anar kalmar ba tare da karanta ta ba.
- Sauran ɗalibai za su canki wace kalma ce ake kwatantawa. A maimata da wasu ɗalibai na daban.

**Gwaji**

4. **Labari a kan ranakun mako** (Minti 10)

Ⓜ • **Ka/ki ce**: *A yau za mu karanta wani labari. Ku buɗe littafinku zuwa shafi na **49**.*

Ⓜ︎Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Me kuka gani a cikin hoton*?

- **Ka/ki ce:** *Me kuke tunanin labarin zai ƙunsa?*
- **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomi kuka gane?*

Ⓓ • Karanta wa ɗalibai labarin sau ɗaya.

- Sake karanta labarin a bayyane. Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu a duk lokacin da suka ji kalmar aiki.

**Bayyanawa**

✓ 5. Auna fahimta (Minti 5)

**Ka/ki ce:**

- ***Wa ke wanke kayan makaranta a ranar Asabar?***
- ***Me Jummai ke yi a ranar Talata da kuma Laraba?***
- ***Me da me ku ke yi a cikin mako?***

**Aikin Gida**

Nemi ɗalibai da su ba 'yan'uwansu ko abokai labarin da aka karanto musu.

**Manufofi:** Ɗalibai za su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki, su kuma kwaikwayi labari.
**Kayan aiki:** Littafin ɗalibai **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (minti 5)

Ⓜ︎Ⓓ • R era waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

## Koyo

2. Kalmomin aiki (minti 10):

Ⓜ︎Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomin aiki muka koya a darasin jiya?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta dukkanin kalmomin, su kuma kwatantasu.

• Kira ɗaya daga cikin ɗalibai gaban aji, domin zaɓen kalma ɗaya a kwatanta ta ba tare da karanta kalmar ba. Maimaita da waɗansu ɗaliban na daban.

3. Baƙin kalmomi (minti 5):

Ⓜ︎ • Rubuta: **[maƙwaɓta]**

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su ba da ma'anar kalmar tare da misalai. A taimakawa ɗalibai idan sun kasa.

Ⓓ • A tambayi ɗalibai muhimmancin **maƙwaɓta**.

## Gwaji

5. Labari a ranakun mako (minti 10)

Ⓓ • Um urci ɗalibai da su ba da labarin da aka karanto a darasin da ya gabata.

Ⓜ︎Ⓓ • Kira ɗalibai domin su kwatanta abin da ke faruwa a labarin, yayin da ka/kike sake karanta labarin.

• Kira waɗansu ɗaliban na daban domin su ma su kwatanta abin da ke faruwa a labarin yayin da ka/kike karantawa.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin aiki da ke cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (minti 10)

**Ka/ki ce:**

- ***Wa ke wanke kayan makaranta a ranar Asabar?***
- ***Me Jummai ke yi a ranar Talata da kuma Laraba?***
- ***Me da me ku ke yi a cikin mako?***

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su zana hoton labarin a littafansu na rubutu.

| No. 35 | Zango na 2 | Mako na 12 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

Manufofi: Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar jarrabawar koyon karatu.
Kayan Aiki: Littafin ɗaukar bayanai da takardar karatu. Lokaci: Minti 35

**JARRABAWA**

Kira ɗalibai ɗaya bayan ɗaya, a yi musu tambayoyi sannan a rubuta sakamakon kowannensu a littafin ɗaukar bayanai. Idan da buƙata, ka/ki nemi tallafi daga Shugaban Makaranta ko 'yan kwamitin 'SBMC' ko daga sauran malamai domin tafiyar da aikin.

Ba wa sauran ɗalibai wani aiki yayin da suke jiran a yi musu jarrabawar. Alal-misali, za a iya ba ɗalibai wani abu su rubuta domin ƙara ƙwarewa wajen rubutu, ko su zana waɗansu abubuwa.

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan haruffa (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**L c sh F H**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan gaɓoɓin kalma (A bayar da maki ɗaya kan kowace gaɓar kalma da aka karanta daidai)

**ci lu fa hu shi**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan kalmomi (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**hula abinci dafa shayi langa**

# Zango na 2, Mako na 12 – Jarrabawar ƙarshen Zango

| Jaha: | | Karamar Hukuma: | | Makaranta: | | Wata: | | Shekara: | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|

| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Bukata ta Musamman (Eh/A'a) | Haruffa | Gaɓar Kalma | Kalma | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /5 | /5 | /5 | / 15 |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |

# Zango na 3

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **[Ɗ ɗ]**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 5)

- (M) Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- (MD) Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- (D) Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Ɗ ɗ

- (M) Rubuta **[Ɗ ɗ]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin [Ɗ].*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***[Ɗ]****, kamar a cikin kalmar* ***[ɗanɗano. Ɗanɗano, ɗanɗano, ɗanɗano!]***
- (MD) Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.
- (D) Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[52]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Ɗaiba da Ɗahiru*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***[Ɗ]****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[Ɗ]** da ke ciki.

## Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



- (M) Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **[Ɗ ɗ]** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.
- (MD) Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.
- (D) Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[Ɗ ɗ]** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Ɗ ɗ]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 6)

Ɗ ɗ

Ⓜ • Rubuta **[Ɗ ɗ]** a kan allo.

ⓂⒹ • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***[Ɗ]****, kamar a cikin kalmar:* ***[ɗanɗano. Ɗanɗano, ɗanɗano, ɗanɗano!]***

• **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***[Ɗ]****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*

Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***[ɗaki]*** *na farawa da harafin* ***[ɗ]****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***[ɗ]****?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[ɗ]** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 15)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.

• Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Ɗ]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[ɗ]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.

• Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

• Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.

• Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.

• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 3 | Mako na 1 | Darasi na 3 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[Ɗ]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
• Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Ɗ]** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜ︎Ⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"ɗa"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **takalmi, ɗalibai, ɗaki, shinkafa, ɗaya**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[52]***.
• Rubuta: **[ɗa]**
• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
Ⓜ︎Ⓓ • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
Ⓜ • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[ɗi, ɗin].**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

Ⓜ︎Ⓓ • Nuna katuna ɗauke da haruffan **[ɗ]** da **[a]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi. | ɗ | a |
• Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[52]***.
• Rubuta: **[ɗaya]**
• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da **[kuɗi, ɗinki]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

**Bayyanawa**

7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 3 | Mako na 1 | Darasi na 4 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[Ɗ]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

ⓂⒹ
- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Ɗ]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

ⓂⒹ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **ɗa, ɗari, ɗaukaka, ɗauri**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| ɗa | ya |
| ku | ɗi |

Ⓜ
- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

## Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ
- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[ɗaya].**

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

Ⓜ
- Maimaita waɗannan matakan da kalmomin **[kuɗi, ɗinki].**

## Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

ⓂⒹ
- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 3 | Mako na 1 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙar Haruffa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

**Bita**

2. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜ︎Ⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| i ɗ | ɗa ɗin |
| Ɗ l | ɗin ɗi |

| | |
|---|---|
| ɗaya | ɗaya |
| kuɗi | ɗinki |

**Saurare**

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

**Bayyanawa**

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

**Aikin Gida**

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 6 | Zango na 3 Mako na 2 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[J j]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙar (Minti 3)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

J j

Ⓜ • Rubuta **[J j]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***[J].***
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***[J]****, kamar a cikin kalmar* ***[ji. Ji, ji, ji!]***

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[54]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Jamila da Junaidu*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***[J]****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[J]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 14)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[J]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[j]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[J j]** da wake ko duwatsu a gida.

## No. 7 | Zango na 3 Mako na 2 Darasi na 2

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[E e]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

E e

Ⓜ • Rubuta **[E e]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***[E]***.
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***[E]****, kamar a cikin kalmar* ***[eeh. Eeh, eeh, eeh!]***

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[54]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***[eeh]*** *na farawa da harafin* ***[e]****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***[e]****?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[e]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 14)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[E]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[e]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[J]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

• Umurci ɗalibai da su gano harafin **[J]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"je"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **jerawa, jemage, ruwa, jeri, ƙasa**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[54]***.

• Rubuta: **[je]**

• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.

Ⓜⓓ • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.

Ⓜ • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[ji, ja].**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

Ⓜⓓ • Nuna katuna ɗauke da haruffan **[j]** da **[e]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi. | j | e |

• Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.

Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaboɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[54]***.

• Rubuta: **[kujera]**

• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da **[jiki, jaki]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

**Bayyanawa**

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*

• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 3 | Mako na 2 | Darasi na 4 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[J]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ
- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **[J]** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

**Koyo**

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

Ⓜ︎Ⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **jere, jirgi, jemage, jekadiya**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| ji | ki |
|---|---|
| ja | je |

Ⓜ︎
- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

**Gwaji**

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ︎
- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[jaki].**

Ⓓ
- Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
- Maimaita waɗannan matakan da kalmar **[jiki, kujera].**

**Bayyanawa**

6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

Ⓜ︎Ⓓ
- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 3 | Mako na 2 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| J j | la lan |
| e E | lu lu |

| | |
|---|---|
| jiki | kujera |
| jaki | jiki |

### Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a ciki. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

| No. 6 | Zango na 3 | Mako na 3 | Darasi na 1 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **[O o]**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 10)

O o

Ⓜ • Rubuta **[O o]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **[O]**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **[O]**, kamar a cikin kalmar **[oho. Oho, oho, oho!]***

(MD) • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[56]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- **Ka/ki ce:** *Kalmar **[omo]** na farawa da harafin **[o]**. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin **[o]**?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[o]** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **[O o]** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD) • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[O o]** da wake ko duwatsu a gida.

## No. 7 | Zango na 3 Mako na 3 Darasi na 2

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[O o]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- (MD) Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- (D) Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

O o

- (M) Rubuta **[O o]** a kan allo.
- (MD) **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* **[O]**, *kamar a cikin kalmar:* ***[oho. Oho, oho, oho!]***
- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* **[O]**. *A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***[omo]*** *na farawa da harafin* **[o]**. *Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* **[o]**?
- (D) Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[o]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- (M) Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[O]** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- (MD) Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- (D) Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Maimaita waɗannan matakan da harafin **[o]**.
- (M) Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- (D) Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**No. 8 | Zango na 3 Mako na 3 Darasi na 3**

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[O]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
• Umurci ɗalibai da su gano harafin **[O]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"ro"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **romo, makaranta, rowa, langa, roro**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[56]***.
• Rubuta: **[no]**
• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
Ⓜⓓ • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
Ⓜ • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[do, lo].**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

| n | o |
|---|---|

Ⓜⓓ • Nuna katuna ɗauke da haruffan **[n]** da **[o]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
• Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[56]****.*
• Rubuta: **[noma]**
• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da **[doro, yalo]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

**Bayyanawa**

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 3 Mako na 3 Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[O]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

ⓂⒹ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su gano harafin **[O]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

ⓂⒹ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **omo, oyoyo, oho**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| no | ma |
| do | ro |

Ⓜ • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa .

• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[noma].**

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da kalmomin **[doro, yalo].**

### Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.

• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

ⓂⒹ • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?

• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?

• **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 9 | Zango na 3 | Mako na 3 | Darasi na 5

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- (MD) Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- (D) Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

- (MD) **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*
- Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.
- (MD) Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.
- (D) Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| O o | no do |
| A a | lo no |

| | |
|---|---|
| doro | noma |
| yalo | doro |

### Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

- (M) Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.
- Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.
- Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

- A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.
- A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.
- A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

- Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.
- Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 6 | Zango na 3 Mako na 4 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **[Z z]**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
• Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Z z

Ⓜ • Rubuta **[Z z]** a kan allo.
• **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***[Z]****.*
• A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***[Z]****, kamar a cikin kalmar* ***[zane. Zane, zane, zane!]***

(MD) • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
• Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[58]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
• ***Ka/ki ce****: Sunayen* ***Zahra'u da Zubairu*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***[Z]****?*
• Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[Z]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **[Z z]** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD) • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
• Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[Z z]** da wake ko duwatsu a gida.

| No. 7 | Zango na 3 | Mako na 4 | Darasi na 2 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Z z]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- Ⓜ️Ⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

Z z

- Ⓜ Rubuta **[Z z]** a kan allo.
- Ⓜ️Ⓓ **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* **[Z]***, kamar a cikin kalmar:* ***[zane. Zane, zane, zane!]***
- **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* **[Z]***. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*
- Ⓓ **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***[zomo]*** *na farawa da harafin* **[z]***. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* **[z]***?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[z]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

- Ⓜ Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Z]** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- Ⓜ️Ⓓ Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- Ⓓ Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Ⓜ Maimaita waɗannan matakan da harafin **[z]**.
- Ⓓ Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[Z]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Z]** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"za"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **niya, zakara, saniya, zaki, zane**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[58]***.
- Rubuta: **[zo]**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[za, bo].**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

Z O

- Nuna katuna ɗauke da haruffan **[z]** da **[o]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[58]***.
- Rubuta: **[zomo]**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- Maimaita waɗannan matakan da **[zabo, zakara]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

**Bayyanawa**

7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[Z]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Z]** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaboɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **zabarmawa, zo, zane, zakara**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| | |
|---|---|
| zo | za |
| mo | bo |

- Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa .
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

## Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

- Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[zomo].**
- Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
- Maimaita waɗannan matakan da kalmomin **[zabo, zakara].**

## Bayyanawa

6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 3 | Mako na 4 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

(MD) • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

(D) • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| Z O | bo bo |
| o z | zo za |

| | |
|---|---|
| zabo | zakara |
| zomo | zomo |

## Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

(M) • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 6 | Zango na 3 Mako na 5 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **[K ƙ]**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
• Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

K ƙ

Ⓜ • Rubuta **[K ƙ]** a kan allo.
• **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **[K]**.*
• A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **[K]**, kamar a cikin kalmar **[ƙirga. Kirga, ƙirga, ƙirga!]***

(MD) • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
• Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[60]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
• ***Ka/ki ce**: Sunan **Kasimu** na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin **[K]**?*
• Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[K]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **[K ƙ]** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD) • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
• Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
• Idan akwai sauran lokaci, a zabi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[K ƙ]** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Ƙ ƙ]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci**:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 6)

Ƙ ƙ

Ⓜ • Rubuta **[Ƙ ƙ]** a kan allo.

Ⓜ︎Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***[Ƙ]****, kamar a cikin kalmar:* ***[ƙirga. Kirga, ƙirga, ƙirga!]***

• **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***[Ƙ]****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*

• **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***[ƙashi]*** *na farawa da harafin* ***[ƙ]****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***[ƙ]****?*

Ⓓ • Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[ƙ]** da ke ciki.

## Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 15)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.

• Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Ƙ]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[ƙ]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.

• Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

• Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.

• Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.

• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 3 | Mako na 5 | Darasi na 3

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[Ƙ]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
• Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Ƙ]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"ƙo"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **korafi, ƙoƙo, riga, wando, danƙo**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[60]***.
• Rubuta: **[ƙu]**
• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
Ⓜⓓ • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
Ⓜ • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[ƙa, ra].**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| ƙ | u |
|---|---|

Ⓜⓓ • Nuna katuna ɗauke da haruffan **[ƙ]** da **[u]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
• Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[60]****.*
• Rubuta: **[ƙura]**
• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da **[ƙusa, tuƙa]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Bayyanawa

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 3 — Mako na 5 — Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[Ƙ]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune — **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

(D) • Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Ƙ]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **kuruciya, ƙusa, ƙarami, ƙura**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| ƙu | ra |
|---|---|
| sa | ƙa |

(M) • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
- Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

(D) • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

(M) • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[ƙura].**

(D) • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
- Maimaita waɗannan matakan da kalmomin **[ƙusa, tuƙa].**

### Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

(MD) • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
- **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
- **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 3 | Mako na 5 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| ƙ | U |
| u | K |

| | |
|---|---|
| ƙa | ƙu |
| ƙu | ra |

| | |
|---|---|
| ƙura | tuƙa |
| ƙusa | ƙura |

### Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

6. Auna fahimta (Minti 7)

✓ • A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 31 | Zango na 3 — Mako na 6 — Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su karanta da kuma rubuta haruffan Ɗ ɗ J j E e O o Z z Ƙ ƙ
**Kayan aiki:** Fensira da littafan rubutu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (minti 5)

- Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.
- Faɗi wasu haruffa da ɗalibai suka koya, a umurce su da su nuna su a cikin waƙar.

### Bita

2. Bitar haruffa (minti 12)

**Ɗɗ Jj Ee Oo Zz Ƙƙ**

- Ⓜ • Rubuta waɗannan haruffan a kan allo:
  Ɗ ɗ J j E e O o Z z K ƙ
- Ⓓ • **Ka/ki ce:** *A yau zamu yi gwaji da bitar haruffan da muka koya a baya.*
- Nuna kowane harafi a jere. Umurci ɗalibai su karanta kuma su nuna harafin. Ba ɗalibai dama su faɗi sunan harafin kafin ka/ki karanta.
- Nuna harruffan ba a cikin jeri ba, sannan a umurci ɗalibai da su karanta su.
- Umurci ɗalibai su yi motsin jikin kowane harafin.
- Umurci ɗalibai su faɗi sunayen da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allo.
- Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allon.

### Gwaji

3. Rubutu (minti 13)

- Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo. Rubuta manya da ƙananan haruffan guda shida. Yi bayanin matakan da ake bi yayin rubutun. Yi wa ɗalibai bayani cewa tsayin ƙaramin harafi yakan kasance rabin babban harafin.
- Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a cikin littafan rubutunsu. Zagaya domin ba su taimako.

### Bayyanawa

✓ 4. Bayyana fahimta (minti 5)

- Nuna wa ɗalibai rubutun ‘yan uwansu da suka yi da kyau, a kuma yi musu bayanin dalilin da ya sa rubutun ya yi kyau.
- Furta sunan harafi. Umurci ɗalibai da su nuna shi a cikin littafin rubutunsu. Maimata hakan da sauran haruffan.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su sake rubuta haruffan a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No.32 | Zango na 3 Mako na 6 Darasi na 2

**Manufa:** Ɗalibai za su karanta gaɓoɓin kalma da kalmomin da ke ɗauke da haruffan **Ɗ J E O Z K**

**Kayan aiki:** Littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (minti 3)

Ⓜ️D • Rera waƙar da ɗalibai tare da motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (minti 4)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kamala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

2. Gwaji da bita (minti 7):

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar karatun gaɓoɓin kalma da kuma kalmomi.*

- Rubuta rukunin gaɓoɓin kalma da kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla gaɓar kalma ko kalma ɗaya na da 'yar'uwa a cikin akwatin.

Ⓓ • Nuna kowace sannan a nemi ɗalibai da su karanta su.

- Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | | |
|---|---|---|
| zo | je | no |
| je | ƙu | ɗa |

| | | |
|---|---|---|
| jiki | ƙaya | noma |
| ƙusa | zomo | ƙaya |

**Gwaji**

5. Katunan nune: dukkan aji (minti 5)

ⓂD • Nuna katunan nune. Umurci ɗalibai su karanta gaɓar da ke jiki.

Ⓓ • Haɗa katunan, domin samar da kalma. Umurci ɗalibai da su karanta kalmar da aka samar.

- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu a gaban aji, su haɗa kalmomi daga katunan.

6. Katunan nune: ƙananan rukunai (minti 10)

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su zauna a cikin ƙananan rukunai. Raba wa kowane rukuni ƙananan takardu guda huɗu masu ɗauke da gaɓoɓin kalma. A umurce su da su haɗa kalmomi daga katunan.

**Bayyanawa**

✓ 7. Bayyana fahimta (minti 5)

Umurci kowane rukuni da ya gabatar da kalma ɗaya da ya haɗa daga katunan nune.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta kalmomi huɗu a cikin littafan rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki su kuma saurari labari.

**Kayan Aiki:** Littafin karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- Rera waƙar da ɗalibai tare da nuna kalmomin waƙar.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmomin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

## Koyo

3. Kalmomin aiki (Minti 10)

- Rubuta: **tashi dafa ci wanke-wanke shirya kula**
- Ka/ki ce: *Yau za mu koyi kalmomin aiki. Za mu karanta kowace kalma tare. Bayan mun karanta kowace kalma, za ku kwatanta aiwatar da ma'anar wannan kalmar.*
- Umurci ɗalibai da su miƙe tsaye. A tallafa musu yadda za su aiwatar da ma'anar kowacce kalma.
- Kira ɗaya daga cikin ɗaliban zuwa gaban allo. Umurci da ya/ta zaɓi kalma ɗaya daga cikin jerin kalmomin ya/ta aiwatar da ma'anar kalmar ba tare da karanta ta ba.
- Sauran ɗalibai za su canki wace kalma ce ake kwatantawa. A maimata da wasu ɗalibai na daban.

## Gwaji

4. **Labari a kan kula da iyali** (Minti 10)

- **Ka/ki ce**: *A yau za mu karanta wani labari. Ku buɗe littafinku zuwa shafi na **62**.*
- **Ka/ki ce:** *Me kuka gani a cikin hoton*?
- **Ka/ki ce:** *Me kuke tunanin labarin zai ƙunsa?*
- **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomi kuka gane?*
- Karanta wa ɗalibai labarin sau ɗaya.
- Sake karanta labarin a bayyane. Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu a duk lokacin da suka ji kalmar aiki.

## Bayyanawa

5. Auna fahimta (Minti 5)

**Ka/ki ce:**

- ***Wa ya tashi da safe?***
- ***Me Mama ta yi?***
- ***Ta yaya kuke taimakawa a gida?***

## Aikin Gida

Nemi ɗalibai da su ba 'yan'uwansu ko abokai labarin da aka karanto musu.

**Manufofi:** Ɗalibai za su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki, su kuma kwaikwayi labari.

**Kayan aiki:** Littafin ɗalibai **Lokaci:** minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (minti 5)

Ⓜⓓ • R era waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

**Koyo**

2. Kalmomin aiki (minti 10):

Ⓜⓓ • **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomin aiki muka koya a darasin jiya?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta dukkanin kalmomin, su kuma kwatantasu.

• Kira ɗaya daga cikin ɗalibai gaban aji, domin zaɓen kalma ɗaya a kwatanta ta ba tare da karanta kalmar ba. Maimaita da waɗansu ɗaliban na daban.

3. Baƙin kalmomi (minti 5):

Ⓜ • Rubuta: **[iyali]**

Ⓜⓓ • Umurci ɗalibai da su ba da ma'anar kalmar tare da misalai. A taimakawa ɗalibai idan sun kasa.

Ⓓ • A tambayi ɗalibai muhimmancin **iyali**.

**Gwaji**

5. Labari a kan kula da iyali (minti 10)

Ⓓ • Um urci ɗalibai da su ba da labarin da aka karanto a darasin da ya gabata.

Ⓜⓓ • Kira ɗalibai domin su kwatanta abin da ke faruwa a labarin, yayin da ka/kike sake karanta labarin.

• Kira waɗansu ɗaliban na daban domin su ma su kwatanta abin da ke faruwa a labarin yayin da ka/kike karantawa.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin aiki da ke cikin labarin.

**Bayyanawa**

✓ 6. Auna fahimta (minti 10)

**Ka/ki ce:**

- ***Wa ya tashi da safe?***
- ***Me Mama ta yi?***
- ***Ta yaya kuke taimakawa a gida?***

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su zana hoton labarin a littafansu na rubutu.

| No. 35 | Zango na 3 | Mako na 6 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

Manufofi: Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar jarrabawar koyon karatu.
Kayan Aiki: Littafin ɗaukar bayanai da takardar karatu. Lokaci: Minti 35

**JARRABAWA**

Kira ɗalibai ɗaya bayan ɗaya, a yi musu tambayoyi sannan a rubuta sakamakon kowannensu a littafin ɗaukar bayanai. Idan da buƙata, ka/ki nemi tallafi daga Shugaban Makaranta ko 'yan kwamitin 'SBMC' ko daga sauran malamai domin tafiyar da aikin.

Ba wa sauran ɗalibai wani aiki yayin da suke jiran a yi musu jarrabawar. Alal-misali, za a iya ba ɗalibai wani abu su rubuta domin ƙara ƙwarewa wajen rubutu, ko su zana waɗansu abubuwa.

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan haruffa (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**ɗ J z ƙ o**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan gaɓoɓin kalma (A bayar da maki ɗaya kan kowace gaɓar kalma da aka karanta daidai)

**je ƙu ɗa zo ja**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan kalmomi (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**tuƙa kujera noma zomo kuɗi**

# Zango na 3, Mako na 6 – Jarrabawar tsakiyar Zango

| Jaha: | | Karamar Hukuma: | | Makaranta: | | Wata: | | Shekara: | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|

| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Bukata ta Musamman (Eh/A’a) | Haruffa | Gaɓar Kalma | Kalma | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /5 | /5 | /5 | / 15 |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |

## No. 6 | Zango na 3 Mako na 7 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Kw ƙw]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Kw ƙw

Ⓜ • Rubuta **[Kw ƙw]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **[Kw]**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **[Kw]**, kamar a cikin kalmar **[ƙwaƙwaƙwa. Kwaƙwaƙwa, ƙwaƙwaƙwa, ƙwaƙwaƙwa!]***

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[64]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- **Ka/ki ce:** *Kalmar **[ƙwarya]** na farawa da harafin **[ƙw]**. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin **[ƙw]**?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[ƙw]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 14)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Kw]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[ƙw]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)
- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[Kw ƙw]** da wake ko duwatsu a gida.

## No. 7 | Zango na 3 Mako na 7 Darasi na 2

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Ai ai]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- (MD) Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- (D) Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

(✓) 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Ai ɑi

- (M) Rubuta **[Ai ai]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***[Ai]***.
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***[Ai]****, kamar a cikin kalmar* ***[aiki. Aiki, aiki, aiki!]***
- (MD) Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.
- (D) Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[64]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunan* ***Aina'u*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***[Ai]****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[Ai]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 14)

- (M) Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Ai]** tare da yin bayanin matakan rubutun.
- (MD) Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.
- (D) Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- (M) Maimaita waɗannan matakan da harafin **[ai]**.
- (D) Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

(✓) 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[Kw]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Kw]** a cikin waƙar.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

**Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"ƙwa"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **kwaƙwaƙwa, ƙwarai, rawa, daka, ƙwaro**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[64]***.
- Rubuta: **[ƙwa]**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[ƙwar, rai].**

**Gwaji**

5. Katunan nune (Minti 7)

| ƙw | a |
|---|---|

- Nuna katuna ɗauke da haruffan **[kw]** da **[a]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[64]***.
- Rubuta: **[ƙwai]**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- Maimaita waɗannan matakan da **[ƙwarya, ƙwarai]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

**Bayyanawa**

7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 8 | Zango na 3 | Mako na 7 | Darasi na 4 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[Kw]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Kw]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*:
**ƙwarya, ƙwarewa, ƙwai, ƙwari**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| ƙwar | ƙwa |
|---|---|
| rai | ya |

Ⓜ • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

## Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[ƙwarai].**
Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da kalmar **[ƙwai, ƙwarya].**

## Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

Ⓜⓓ • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
• **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 9 | Zango na 3 | Mako na 7 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ️Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Bita

3. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜ️Ⓓ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| ƙw | ai |
| Ai | ƙw |

| | |
|---|---|
| ƙwar | ƙwa |
| ƙwa | rai |

| | |
|---|---|
| ƙwarya | ƙwarya |
| ƙwai | ƙwarai |

## Saurare

4. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

## Bayyanawa

✓ 5. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a ciki. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

## Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "karin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **[Kw kw]**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 5)

Ⓜ
- Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ
- Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

## Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Kw kw

Ⓜ
- Rubuta **[Kw kw]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **[Kw]**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **[Kw]**, kamar a cikin kalmar **[kwalliya. Kwalliya, kwalliya, kwalliya!]***

ⓂⒹ
- Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[66]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- **Ka/ki ce:** *Kalmar **[kwalliya]** na farawa da harafin **[kw]**. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin **[kw]**?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[kw]** da ke ciki.

## Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)

Kw kw

Ⓜ
- Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **[Kw kw]** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

ⓂⒹ
- Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.
- Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

## Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[Kw kw]** da wake ko duwatsu a gida.

| No. 7 | Zango na 3 | Mako na 8 | Darasi na 2 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Kw kw]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu    Lokaci: Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 6)

Kw kw

Ⓜ • Rubuta **[Kw kw]** a kan allo.

Ⓜ︎Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***[Kw]****, kamar a cikin kalmar:* ***[kwalliya. Kwalliya, kwalliya, kwalliya!]***

• **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***[Kw]****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*

Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***[kwakwa]*** *na farawa da harafin* ***[kw]****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***[kw]****?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[kw]** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 15)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.

• Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Kw]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[kw]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.

• Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 10)

• Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.
• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

## No.8 | Zango na 3 Mako na 8 Darasi na 3

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[Kw]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.
- Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Kw]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

ⓂⒹ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* **"kwai"** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **bishiya, kwaikwayo, aski, akwai, bakwai**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

- Ⓜ **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[66]***.
- Rubuta: **[kwa]**
- Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.
- ⓂⒹ Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.
- Ⓜ A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[kwai, yo].**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| kw | ai |
|---|---|

- ⓂⒹ Nuna katuna ɗauke da haruffan **[kw]** da **[ai]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.
- Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.
- Ⓓ Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

- Ⓜ **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[66]***.
- Rubuta: **[kwakwa]**
- Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.
- Ⓓ Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.
- Ⓜ Maimaita waɗannan matakan da **[akwai, kwaikwayo, kwando]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Bayyanawa

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

- **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*
- Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No.8 | Zango na 3 — Mako na 8 — Darasi na 4

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[Kw]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Kw]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓobin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **kwabbai, kwaikwayo, kwalba, kwalliya.**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| kwa | kwa |
|---|---|
| kwan | do |

Ⓜ • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa .
• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

### Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

Ⓜ • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[akwai].**

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da kalmomin **[kwakwa, kwando].**

### Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

Ⓜⓓ • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
• **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No.9 | Zango na 3 | Mako na 8 | Darasi na 5 |
|---|---|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

**Bita**

3. Bita da gwaji (Minti 12)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

Ⓜ • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

Ⓓ • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| Kw ai | kwa yo |
| kw Ai | kwai kwai |

| | |
|---|---|
| kwakwa | kwaikwayo |
| akwai | kwakwa |

**Saurare**

4. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

Ⓜ • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

**Bayyanawa**

5. Auna fahimta (Minti 7)

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

**Aikin Gida**

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Gw gw]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

ⓂⒹ • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 10)

Gw gw

Ⓜ • Rubuta **[Gw gw]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **[Gw]**.*
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **[Gw]**, kamar a cikin kalmar **[gwalo. Gwalo, gwalo, gwalo!]***

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[68]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- **Ka/ki ce:** *Kalmar **[gwanda]** na farawa da harafin **[gw]**. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin **[gw]**?*
- Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[gw]** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 14)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Gw]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Maimaita waɗannan matakan da harafin **[gw]**.
- Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

- Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[Gw gw]** da wake ko duwatsu a gida.

## No.7 | Zango na 3 — Mako na 9 — Darasi na 2

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Au au]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu — Lokaci: Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Au au

Ⓜ • Rubuta **[Au au]** a kan allo.
- **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin* ***[Au].***
- A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin* ***[Au]****, kamar a cikin kalmar* ***[auna. Auna, auna, auna!]***

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.
- Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[68]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.
- ***Ka/ki ce****: Sunan* ***Auwal*** *na farawa da wannan harafin. Ko za ku iya tuna wani suna da ke farawa da harafin* ***[Au]****?*
- Rubuta sunayen da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta sunan, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[Au]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Rubutun harafi (Minti 14)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.
- Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Au]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

Ⓜ︎Ⓓ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.
- Maimaita waɗannan matakan da harafin **[au]**.
- Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.
- Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)
- Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.
- Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
- Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

| No.8 | Zango na 3 | Mako na 9 | Darasi na 3 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[Gw]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

• Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Gw]** a cikin waƙar.

(✓) 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"gwa"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **kwalliya, gwagwarmaya, agwagwa, gwani, lemo**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[68]***.

• Rubuta: **[gwau]**

• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.

(MD) • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.

(M) • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[gwai, gwa].**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

(MD) • Nuna katuna ɗauke da haruffan **[gw]** da **[au]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.

gw | au

• Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.

(D) • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaɓoɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[68]***.

• Rubuta: **[gwauro]**

• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.

(D) • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.

(M) • Maimaita waɗannan matakan da **[gwaiba, agwagwa]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Bayyanawa

(✓) 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*

• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No.8 | Zango na 3 | Mako na 9 | Darasi na 4 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[Gw]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.

(D) • Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Gw]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Koyo

*3. Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓobin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **gwaza, gwaiba, gwiwa, gwagwarmaya**

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

| gwai | ba |
|---|---|
| gwau | ro |

(M) • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.

(D) • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

## Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

(M) • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[gwauro].**

(D) • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.

(M) • Maimaita waɗannan matakan da kalmar **[gwaiba, gwanda].**

## Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

(MD) • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
• **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 9 | Zango na 3 | Mako na 9 | Darasi na 5

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

2. Bita da gwaji (Minti 12)

- Ⓜ **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*
- Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.
- Ⓜ︎Ⓓ Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.
- Ⓓ Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | |
|---|---|
| Gw gw | au Au |

| | |
|---|---|
| gwau gwai | gwa gwau |

| | |
|---|---|
| gwaiba gwauro | agwagwa gwaiba |

### Saurare

5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)

- Ⓜ Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.
- Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.
- Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ 6. Auna fahimta (Minti 7)

- A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.
- A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.
- A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a ciki. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

- Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.
- Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

## No. 6 | Zango na 3 Mako na 10 Darasi na 1

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane harafin **[Ɓ ɓ]**, kuma su iya jera wake ko duwatsu wajen haɗa harafin.

**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma wake ko duwatsu **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 5)

Ⓜ • Rera waƙar tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

• Rera waƙar yayin da ka/kike nuna kalmomin.

(MD) • Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 5)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. A bayar da sakamako da ƙarfafa gwiwa.

### Koyo

3. Sunan harafi (Minti 10)

Ɓ ɓ

Ⓜ • Rubuta **[Ɓ ɓ]** a kan allo.

• **Ka/ki ce:** A *yau za mu koyi harafin **[Ɓ]**.*

• A nuna harafin sannan a faɗi sunansa sau uku*: Sunan harafin **[Ɓ]**, kamar a cikin kalmar **[bare. Ɓare, bare, bare!]***

(MD) • Umurci ɗalibai da ku yi motsin jikin harafin tare.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su yi motsin jikin harafin su kaɗai.

• Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen akwati a shafi na **[70]** cikin littafinsu. Umurce su da su nuna harafin su kuma maimaita furta sunan harafin.

• **Ka/ki ce:** *Kalmar **[ɓera]** na farawa da harafin **[ɓ]**. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin **[ɓ]**?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[ɓ]** da ke ciki.

### Gwaji

4. Haɗa haruffa (Minti 10)



Ⓜ • Nuna wa ɗalibai yadda ake haɗa harafin **[Ɓ ɓ]** da wake ko duwatsu, ta hanyar rubutu a kan allo.

(MD) • Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni wake ko duwatsu.

Ⓓ • Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa babban harafi da waken ko duwatsun.

• Umurci ɗalibai a kowane rukuni su haɗa ƙaramin harafi da waken ko duwatsun.

### Bayyanawa

✓ 5. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Umurci ɗalibai da su duba misalai masu kyau na aikin daga wasu rukunai.

• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari daga cikin kundin labarai, a karantawa ɗalibai.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su haɗa harafin **[Ɓ ɓ]** da wake ko duwatsu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya karantawa da kuma rubuta harafin **[Ɓ ɓ]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da fensira da kuma littafan rubutu Lokaci: Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

ⓂⒹ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

2. Duba aikin gida (Minti 1)

Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu sama idan sun haɗa harafin a gida da wake ko duwatsu. A tafa wa ɗaliban.

**Koyo**

3. Sunan harafi (Minti 6)

Ɓ ɓ

Ⓜ • Rubuta **[Ɓ ɓ]** a kan allo.

ⓂⒹ • **Ka/ki ce:** *Mu yi motsin jikin harafin da muka koya a jiya. Sunan harafin* ***[Ɓ]****, kamar a cikin kalmar:* ***[ɓare. Ɓare, ɓare, ɓare!]***

• **Ka/ki ce:** *Jiya mun yi tunanin sunayen da suka fara da* ***[Ɓ]****. A koyaushe ana amfani da babban harafi wajen rubuta sunaye. Sannan ana amfani da ƙananan haruffa wajen rubuta sauran kalmomi.*

Ⓓ • **Ka/ki ce:** *Kalmar* ***[ɓawo]*** *na farawa da harafin* ***[ɓ]****. Waɗanne kalmomi kuma ke farawa da harafin* ***[ɓ]****?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo. Bayan an rubuta kalmar, sai a nuna wa ɗalibai harafin **[ɓ]** da ke ciki.

**Gwaji**

4. Rubutun harafi (Minti 15)

Ⓜ • Umurci ɗalibai da su buɗe littafan rubutunsu, su kuma ɗauko fensiransu.

• Zana layukan rubutu a kan allo, sannan a rubuta harafin **[Ɓ]** tare da yin bayanin matakan rubutun.

ⓂⒹ • Umurci ɗalibai da su tashi tsaye, su rubuta harafin a iska tare da kai/ke.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su ɗaga fensiransu, sannan su rubuta harafin a cikin littafansu na rubutu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da harafin **[ɓ]**.

Ⓓ • Ɗalibai su rubuta babba da ƙaramin harafin gwargwadon yadda za su iya.

• Zagaya domin taimakawa ɗaliban. Yi musu bayanin cewa za su iya taimaka wa junansu.

**Bayyanawa**

5. Bayyana fahimta (Minti 10)

• Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta.

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.

• Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai da ya/ta rubuta haruffan a kan allo.

• Idan akwai sauran lokaci, a zaɓi wani labari a karanta wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a gida. Su cika layi 3 na littafin rubutunsu.

## No. 8 | Zango na 3 Mako na 10 Darasi na 3

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta gaɓoɓin kalma masu ɗauke da harafin **[Ɓ]**
**Kayan Aiki:** Katunan nune da littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

• Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Ɓ]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

3. Bambance sautukan gaɓoɓi (Minti 2)

Ⓜ︎Ⓓ **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi ɗaya bayan ɗaya. Idan kalmar na da gaɓar* ***"ɓa"*** *to sai ku ɗaga babban yatsanku ya kalli sama. Idan kuma babu, sai babban yatsanku ya kalli ƙasa*: **ɓata, ɓarewa, ɓawo, gida, kogi**

4. Karatun gaɓar kalma (Minti 5)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa haruffa domin mu gina gaɓar kalma. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[70]***.

• Rubuta: **[ɓa]**

• Faɗi sunan kowane harafi a wannan gaɓar, sannan ka/ki karanta ta.

Ⓜ︎Ⓓ • Jagoranci ɗalibai zuwa ga sashen da'ira a cikin littafansu, sai a maimaita matakin da littafin karantun ɗalibai.

Ⓜ • A sake maimaita waɗannan matakan da gaɓoɓin kalmar **[ɓul, ɓe].**

### Gwaji

5. Katunan nune (Minti 7)

| ɓ | e |
|---|---|

Ⓜ︎Ⓓ • Nuna katuna ɗauke da haruffan **[ɓ]** da **[e]**. Umurci ɗalibai su faɗi sunan kowane harafi.

• Haɗa katunan domin samar da gaɓar kalma. Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar da aka samar.

Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da gaɓoɓin kalma don 'yan aji su karanta.

6. Karatun kalma (Minti 10)

Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu haɗa gaboɓin kalma domin mu gina kalmomi. Ku buɗe littafanku zuwa shafi na* ***[70]****.*

• Rubuta: **[ɓata]**

• Nuna kalmar a kan allo. Karanta kowace gaɓa a bayyane, sannan ka/ki karanta kalmar.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta kalmar tare da kai/ke a kan allo da kuma a cikin littafansu.

Ⓜ • Maimaita waɗannan matakan da **[ɓullowa, taɓarya, ɓera]**. Ɗalibai su nuna kalmomin a lokacin da suke karatun.

### Bayyanawa

✓ 7. Bayyana fahimta (Minti 2)

• **Ka/ki ce:** *Zan faɗi wata kalma sai ku nuna ta a cikin littafinku, daga nan sai ku duba amsarku da ta abokan zamanku.*

• Zagaya cikin aji ka/ki duba ayyukansu, yayin da ka/kike faɗin kalmomin.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

**Manufa:** Ɗalibai za su iya karanta kalmomi masu ɗauke da harafin **[Ɓ]**
**Kayan Aiki:** Littafan karatun ɗalibai da kuma katunan nune **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (Minti 3)

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.
• Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin wakar.
(D) • Umurci ɗalibai da su gano harafin **[Ɓ]** a cikin waƙar.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)
Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

## Koyo

3. *Amon* sautin gaɓa (Minti 2)

(MD) **Ka/ki ce:** *Yanzu za mu yi wasan saurare. Zan furta wasu kalmomi, ina so ku tafa yawan gaɓoɓin kalmar, sannan ku nuna yawansu da yatsunku*: **ɓalle, ɓera, ɓangare, ɓanɓarowa**

| ɓa | ta |
|---|---|
| ɓe | ra |

4. Karatun Kalma – katunan nune (Minti 10)

(M) • Nuna katunan nune. Nemi ɗalibai su faɗi sunan kowace gaɓa.
• Haɗa katunan domin samar da kalma. Nemi ɗalibai su karanta kalmar da aka samar.
(D) • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu zuwa gaban aji, su samar da kalmomi daga katunan don 'yan aji su karanta.

## Gwaji

5. Rubutun kalma (Minti 10)

(M) • Zana layukan rubutu a kan allo, sai a rubuta kalmar **[ɓata].**
(D) • Umurci ɗalibai da su rubuta kalmar a cikin littafansu na rubutu. Zagaya domin taimaka wa ɗaliban.
(M) • Maimaita waɗannan matakan da kalmomin **[taɓarya, ɓera].**

## Bayyanawa

✓ 6. Bayyana fahimta (Minti 5)

• Nuna misalin rubutu mai kyau na ɗaya daga cikin ɗalibai. Nemi ɗalibai su gano me ya sa rubutun ya yi kyau.
• Rubuta wata gaɓar kalma a kan allo.Nemi ɗalibai da su karanta gaɓar kalma. Maimaita matakin da wata gaɓar kalma ta daban.

7. Tattaunawa a kan hotuna (Minti 5)

(MD) • **Ka/ki ce:** Ku duba hoton da ke cikin littafanku na karatu. Me ke faruwa a cikin hoton?
• **Ka/ki ce:** Ko ya tuna muku da kalmomin da muka koya? Waɗanne kalmomi ne?
• **Ka/ki ce**: Ko wannan hoton ya tuna muku da wani ɓangare na rayuwarku? Ta yaya?

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su rubuta kalmomin darasin a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

## No. 9 | Zango na 3 Mako na 10 Darasi na 5

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bitar muhimman bayanai da kuma amsa tambayoyi a kan labari.
**Kayan Aiki:** Kundin labaran karatu a bayyane **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

<u>1. Waƙa (Minti 3)</u>

(MD) • Rera waƙar tare da ɗalibai yayin da ake nuna kalmomin.

(D) • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da kwatanta motsin jiki.

✓ <u>2. Duba aikin gida (Minti 3)</u>

Umurci ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin.

### Bita

<u>2. Bita da gwaji (Minti 12)</u>

(M) • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar abubuwan da muka koya a wannan makon.*

• Rubuta rukuni na haruffa da gaɓoɓi da kuma kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla harafi ko gaɓa ko kalma ɗaya na da ɗan'uwa a cikin akwatin.

(MD) • Nuna kowane sannan a nemi ɗalibai su karanta su.

(D) • Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| Ɓ a | ɓe ɓe |
|---|---|
| A ɓ | ɓul ɓa |

ɓera ɓera
ɓata taɓarya

### Saurare

<u>5. Karatun labari a bayyane (Minti 10)</u>

(M) • Zaɓi labari daga cikin kundin labarai. Karanta taken, sannan ka/ki nuna hoto, sai a tambayi ɗalibai su yi hasashen abun da labarin ya ƙunsa.

• Koyar da sababbin kalmomi biyu da aka tura.

• Karanta labarin a bayyane tare da nuna alamomin sosa rai. Tsaya sau ɗaya ko biyu a tambayi ɗalibai a kan abun da suka ji ko kuma abun da suke tunanin zai faru a gaba cikin labarin.

### Bayyanawa

✓ <u>6. Auna fahimta (Minti 7)</u>

• A tambaye su ko hasashensu ya yi daidai.

• A yi wa ɗalibai tambayoyin auna fahimta a kan labarin.

• A tambayi ɗalibai waɗanne sababbin kalmomi suka koya a cikin labarin. Ɗalibai su yi bayanin abun da kalmomin suke nufi kuma su yi amfani da su a cikin jimla.

### Aikin Gida

• Umurci ɗalibai da su bayar da labarin ga wasu abokansu ko kuma 'yan'uwansu a gida.

• Umurci ɗalibai su cika sashen "ƙarin gwaji" a cikin littafin karatunsu tare da taimakon abokansu ko 'yan'uwansu a gida.

**Manufofi:** Ɗalibai za su karanta da kuma rubuta haruffan **Kw ƙw Ai ai Kw kw Gw gw Au au Ɓ ɓ**
**Kayan aiki:** Fensira da littafan rubutu **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

1. Waƙa (minti 5)

- Ⓜⓓ Rera waƙar da ɗalibai tare da kwatanta motsin jikin waƙar.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.
- Fadi wasu haruffa da ɗalibai suka koya, a umurce su da su nuna su a cikin waƙar.

## Bita

2. Bitar haruffa (minti 12)

**Kw ƙw Ai ai Kw kw Gw gw Au au Ɓ ɓ**

- Ⓜ Rubuta waɗannan haruffan a kan allo: **Kw ƙw Ai ai Kw kw Gw gw Au au Ɓ ɓ**
- **Ka/ki ce:** *A yau zamu yi gwaji da bitar haruffan da muka koya a baya.*
- Ⓓ Nuna kowane harafi a jere. Umurci ɗalibai su karanta kuma su nuna harafin. Ba ɗalibai dama su faɗi sunan harafin kafin ka/ki karanta.
- Nuna harruffan ba a cikin jeri ba, sannan a umurci ɗalibai da su karanta su.
- Umurci ɗalibai su yi motsin jikin kowane harafin.
- Umurci ɗalibai su faɗi sunayen da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allo.
- Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin da ke farawa da kowane harafi. A rubuta su a kan allon.

## Gwaji

3. Rubutu (minti 13)

- Ⓜ Zana layukan rubutu a kan allo. Rubuta manya da ƙananan haruffan guda shida. Yi bayanin matakan da ake bi yayin rubutun. Yi wa ɗalibai bayani cewa tsayin ƙaramin harafi yakan kasance rabin babban harafin.
- Ⓓ Umurci ɗalibai da su rubuta haruffan a cikin littafan rubutunsu. Zagaya domin ba su taimako.

## Bayyanawa

✓ 4. Bayyana fahimta (minti 5)

- Nuna wa ɗalibai rubutun 'yan uwansu da suka yi da kyau, a kuma yi musu bayanin dalilin da ya sa rubutun ya yi kyau.
- Furta sunan harafi. Umurci ɗalibai da su nuna shi a cikin littafin rubutunsu. Maimata hakan da sauran haruffan.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su sake rubuta haruffan a gida. Su cika layi uku na littafin rubutunsu.

| No. 32 | Zango na 3 | Mako na 11 | Darasi na 2 |
|---|---|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su karanta gaɓoɓin kalma da kalmomin da ke ɗauke da haruffan **Kw Ai Kw Gw Au Ɓ**

**Kayan aiki:** Littafan karatun ɗalibai **Lokaci:** minti 35

### Fara Darasi

1. Waƙa (minti 3)

- Ⓜ︎Ⓓ • Rera waƙar da ɗalibai tare da motsin jikin waƙar.
- Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

2. Duba aikin gida (minti 4)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kamala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

### Koyo

2. Gwaji da bita (minti 7):

- Ⓜ • **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwaji da bitar karatun gaɓoɓin kalma da kuma kalmomi.*
- Rubuta rukunin gaɓoɓin kalma da kalmomi a kan allo. A tabbatar a ƙalla gaɓar kalma ko kalma ɗaya na da 'yar'uwa a cikin akwatin.
- Ⓓ • Nuna kowace sannan a nemi ɗalibai da su karanta su.
- Kira ɗalibai su zo gaban aji, su ja layi tsakanin waɗanda suke iri ɗaya a cikin kowane akwati.

| | | |
|---|---|---|
| kwai | ƙwa | ƙwar |
| gwau | ɓa | ƙwa |

| | | |
|---|---|---|
| ƙwai | gwaiba | aƙwai |
| gwaiba | aƙwai | ɓera |

### Gwaji

5. Katunan nune: dukkan aji (minti 5)

- Ⓜ︎Ⓓ • Nuna katunan nune. Umurci ɗalibai su karanta gaɓar da ke jiki.
- Haɗa katunan, domin samar da kalma. Umurci ɗalibai da su karanta kalmar da aka samar.
- Ⓓ • Kira ɗalibai su fito a ra'ayin kansu a gaban aji, su haɗa kalmomi daga katunan.

| | |
|---|---|
| ƙwar | rai |
| gwau | ro |

6. Katunan nune: ƙananan rukunai (minti 10)

- Ⓓ • Umurci ɗalibai da su zauna a cikin ƙananan rukunai. Raba wa kowane rukuni ƙananan takardu guda huɗu masu ɗauke da gaɓoɓin kalma. A umurce su da su haɗa kalmomi daga katunan.

### Bayyanawa

7. Bayyana fahimta (minti 5)

Umurci kowane rukuni da ya gabatar da kalma ɗaya da ya haɗa daga katunan nune.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su rubuta kalmomi huɗu a cikin littafan rubutunsu.

**Manufofi:** Ɗalibai su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki su kuma saurari labari.

**Kayan Aiki:** Littafin karatun ɗalibai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (Minti 3)

- Ⓜⓓ Rera waƙar da ɗalibai tare da nuna kalmomin waƙar.
- Ⓓ Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmomin yayin da sauran ɗalibai ke rerawa tare da motsin jiki.

✓ 2. Duba aikin gida (Minti 3)

Umurci ɗalibai da su ɗaga littafansu sama, su nuna aikinsu. Yaba wa ɗaliban da suka kammala aikin, a kuma ƙarfafa musu gwiwa.

**Koyo**

3. Kalmomin aiki (Minti 10)

- Ⓜ Rubuta: **kira aiki sawo kawo murna**
- Ka/ki ce: *Yau za mu koyi kalmomin aiki. Za mu karanta kowace kalma tare. Bayan mun karanta kowace kalma, za ku kwatanta aiwatar da ma'anar wannan kalmar.*
- Ⓜⓓ Umurci ɗalibai da su miƙe tsaye. A tallafa musu yadda za su aiwatar da ma'anar kowacce kalma.
- Ⓓ Kira ɗaya daga cikin ɗaliban zuwa gaban allo. Umurci da ya/ta zaɓi kalma ɗaya daga cikin jerin kalmomin ya/ta aiwatar da ma'anar kalmar ba tare da karanta ta ba.
- Sauran ɗalibai za su canki wace kalma ce ake kwatantawa. A maimata da wasu ɗalibai na daban.

**Gwaji**

4. **Labari a kan magani** (Minti 10)

- Ⓜ **Ka/ki ce**: *A yau za mu karanta wani labari. Ku buɗe littafinku zuwa shafi na **72**.*
- Ⓜⓓ **Ka/ki ce:** *Me kuka gani a cikin hoton*?
- **Ka/ki ce:** *Me kuke tunanin labarin zai ƙunsa?*
- **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomi kuka gane?*
- Karanta wa ɗalibai labarin sau ɗaya.
- Sake karanta labarin a bayyane. Umurci ɗalibai da su ɗaga hannunsu a duk lokacin da suka ji kalmar aiki.

**Bayyanawa**

✓ 5. Auna fahimta (Minti 5)

**Ka/ki ce:**

- **Mene ne Kaka take so?**
- **Me yasa Kaka tayi murna?**
- **Ko kun taɓa taimakon marasa lafiya?**

**Aikin Gida**

Nemi ɗalibai da su ba 'yan'uwansu ko abokai labarin da aka karanto musu.

## No. 34 | Zango na 3 Mako na 11 Darasi na 4

**Manufofi:** Ɗalibai za su kwatanta aiwatar da ma'anar kalmomin aiki, su kuma kwaikwayi labari.
**Kayan aiki:** Littafin ɗalibai **Lokaci:** minti 35

**Fara Darasi**

1. Waƙa (minti 5)

Ⓜⓓ • R era waƙar tare da ɗalibai yayin da ka/kike nuna kalmomin.

Ⓓ • Umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta riƙa nuna kalmonin yayin da sauran ɗalibai ke rera waƙar tare da motsin jiki.

**Koyo**

2. Kalmomin aiki (minti 10):

Ⓜⓓ • **Ka/ki ce:** *Waɗanne kalmomin aiki muka koya a darasin jiya?*

• Rubuta kalmomin da ɗalibai suka bayar a kan allo.

Ⓓ • Umurci ɗalibai da su karanta dukkanin kalmomin, su kuma kwatantasu.

• Kira ɗaya daga cikin ɗalibai gaban aji, domin zaɓen kalma ɗaya a kwatanta ta ba tare da karanta kalmar ba. Maimaita da waɗansu ɗaliban na daban.

3. Baƙin kalmomi (minti 5):

Ⓜ • Rubuta: **[magani]**

Ⓜⓓ • Umurci ɗalibai da su ba da ma'anar kalmar tare da misalai. A taimakawa ɗalibai idan sun kasa.

Ⓓ • A tambayi ɗalibai muhimmancin **magani**.

**Gwaji**

5. Labari a kan magani (minti 10)

Ⓓ • Um urci ɗalibai da su ba da labarin da aka karanto a darasin da ya gabata.

Ⓜⓓ • Kira ɗalibai domin su kwatanta abin da ke faruwa a labarin, yayin da ka/kike sake karanta labarin.

• Kira waɗansu ɗaliban na daban domin su ma su kwatanta abin da ke faruwa a labarin yayin da ka/kike karantawa.

Ⓓ • Umurci ɗalibai su faɗi kalmomin aiki da ke cikin labarin.

**Bayyanawa**

✓ 6. Auna fahimta (minti 10)

**Ka/ki ce:**

- **Mene ne Kaka take so?**
- **Me yasa Kaka tayi murna?**
- **Ko kun taɓa taimakon marasa lafiya?**

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai su zana hoton labarin a littafansu na rubutu.

Manufofi: Manufofi: Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar jarrabawar koyon karatu.

Kayan Aiki: Littafin ɗaukar bayanai da takardar karatu. Lokaci: Minti 35

**JARRABAWA**

Kira ɗalibai ɗaya bayan ɗaya, a yi musu tambayoyi sannan a rubuta sakamakon kowannensu a littafin ɗaukar bayanai. Idan da buƙata, ka/ki nemi tallafi daga Shugaban Makaranta ko 'yan kwamitin 'SBMC' ko daga sauran malamai domin tafiyar da aikin.

Ba wa sauran ɗalibai wani aiki yayin da suke jiran a yi musu jarrabawar. Alal-misali, za a iya ba ɗalibai wani abu su rubuta domin ƙara ƙwarewa wajen rubutu, ko su zana waɗansu abubuwa.

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan haruffa (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**ƙw kw gw au ɓ**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan gaɓoɓin kalma (A bayar da maki ɗaya kan kowace gaɓar kalma da aka karanta daidai)

**kwa kwai gwau ƙwa ɓa**

Umurci ɗalibai da su karanta waɗannan kalmomi (A bayar da maki ɗaya kan kowace kalma da aka karanta daidai)

**ɓera ƙwai agwagwa gwaiba akwai**

# Zango na 3, Mako na 12 – Jarrabawar ƙarshen Zango

| **Jaha:** | | **Karamar Hukuma:** | | **Makaranta:** | | **Wata:** | | **Shekara:** | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|

| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Bukata ta Musamman (Eh/A'a) | Haruffa | Gaɓar Kalma | Kalma | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /5 | /5 | /5 | / 15 |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |

# Waƙoƙi

**Waƙar Gaisuwa**
Idan muka tashi da safe,
Sai mu gai da iyayenmu x2
Mamata ina kwana,
Gaisuwa ce da safe,
Ina wuni Babana,
Gaisuwa ce da rana,
Mamata sai da safe,
Gaisuwa ce da dare.

**Waƙar Haruffa**
a, b, c, d, e, f, g, h!
i, j, k, l, m, n, o, r!
s, t, u, w, y, z!
An taso daga makaranta,
'Yan makaranta na wasa,
Kwallo da langa da sassaka,
Komai girman ɗan boko,
Bai wuce abacada ba!

**Waƙar Ranakun Mako**
Yara, yara 'yan makaranta
A mako muna da kwanaki guda bakwai.
Lahadi muke shiri mu tsaftace tufa.
Litinin mu garzaya mu je makaranta.
Talata da Laraba mu je makaranta.
Alhamis da Juma'a mu je makaranta.
Asabar mu shakata mu je mu yi hutu.
Mu wataya mu rausaya mu je muyi wasa.

**Waƙar Tafa Tafa**
Tafa tafa tafiyar
nan da zamu tare,
Da wa muka zo ne,
Daga malam, sai fa yara,
Yara ku shirya ga malam,
sai karatu.

**Waƙar Gizo**
Gizo gizon zama
gizo ya dawo,
Ana rabon zuma
gizo ya faɗo
Dif!

**Waƙar Tsafta**
Tsafta, Tsafta, Tsafta, Tsafta,
Tsafta,Tsafta,
Wanke hannu, yara shi ne tsafta, tsafta,
Wanke baki, yara shi ne tsafta, tsafta,
Wanka, wanki, yara shi ne tsafta, tsafta,
Tsafta, Tsafta, Tsafta, Tsafta,
Tsafta, Tsafta.

**Waƙar Ɗan Maliyo**
Ɗan maliyo maliyo, ɗa!
Ɗan maliyo nawa, ɗa!
Ya je ina ne, ɗa!
Ya je Ɗan Ali, ɗa!
Ɗan Ali gari ne, ɗa!
Zai ɗau ɗan boto, ɗa!
Ɗaɗɗaga mu gani!
ɗa ɗa ɗa ɗa!

**Waƙar Tantabara**
Tantabara tara,
Kwai tara,
Ɗa tara,
Za ta gari tara,
Inda mutum tara.

**Waƙar Kanƙara**
Kanƙara da damina,
Kwal ƙwal ƙwal,
Ana ruwa da ƙanƙara,
Kwal ƙwal ƙwal,
Kara a kan gidajenmu,
Kwal ƙwal ƙwal,
A kan kwanon makarantarmu,
Kwal ƙwal ƙwal.

**Waƙar Zabuwa**
Zabuwa da zanenta,
Zabo da kora,
Zomo da zararsa,
Zabura ka cin mai,
Zuma da zaƙinta,
Zam zam zam

**Waƙar Kirge (1)**
Ɗaya mafarin ƙirge,
Biyu idanun dabba,
Uku duwatsun murhu,
Huɗu ƙafafun tebur,
Biyar na yatsun hannu.

**Waƙar Kirge (2)**
Ɗaya mafarin ƙirge,
Biyu idanun dabba,
Uku duwatsun murhu,
Huɗu ƙafafun tebur,
Biyar na yatsun hannu.
Shida kwanakin aiki.
Bakwai kwanakin mako.
Takwas goma ba biyu kenan.
Tara daga ke sai goma.
Goma biyar biyu Kenan.

**Waƙar Motsa Jiki**
Yara mu tafa,
Muna ta tafawa,
Mu tashi, muna ta tasawa,
Mu juya, muna ta juyawa,
Mu duƙa, muna ta duƙawa,
Mu zauna, muna ta zaunawa